[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□ *MASARAUTARMU*

□□□□□□□

Story & Writing By _R.Hussain_

&

Noory

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

Wannan littafin *na kud'i ne*

Normal group *N300*

VIP N500

Ki *biya* ki *karanta cikin* *aminci*

2414444137

Zenith *bank*

Rahinat Hussain

Ki tura shedar biya ta wannan number 08107916039

Idan kuma recharge card ne MTN ta wannan numbers 08107916039 kuma 08145498489. Bamason VTU♀

Bismillahir'rahmanurrahim.

 Page 1

.....Garin Duhuwa wa ni gari ne da ke yankin Africa cikin k'asar Gabon

mutanen garin ba su da tufafin sa wa sai walki, Wanda su ke yin sa da fatun dabbobi, da shi suke kare al'aurar su Mazan su da Matan su ba su san wa ni addini ba face bautar K'AININA(K'ainina wa ni dodon tsafin su ne wanda su ke bautar shi) duk shekara ana bikin ba wa k'ainina jinin mutane.

Za'a duba Maza matasa wad'an da su ka girma amma ba su ta b'a kusantar mace ba, to irin wad'annan mazan a ke kamawa guda biyu a yanka su a ba wa k'ainani jinin su da

Naman su za'a yi girkin bikin shekara

Garin tamkar mayu haka su ke.

Duk wa ni bak'o indai hanya ta biyo da shi garin Duhuwa to sunan sa gawa dan sai sun kashe shi bayan sun a zabtar da shi.

Sarkin Garin Duhuwa Gannami k'aton kafuri ne azzalumi ne, in dai ya ga y'ar ka ko matar ka ya ji ta yi ma sa to dole ka rabu da ita ka ba shi ta dad'in rai ko ya kashe ka ya k'wace ta.

'Ya'yan ka su zama k'ask'antattun ba yi in mata ne ya sa su cikin bayin sa, sa d'aka sarki Gannami ya na da d'a guda d'aya Hazid.

Hazid ya taso cikin gata ko wa ya san irin son da sarki Gannami ya ke wa yarima Hazid shi ma ya gaji zalinci mugu ne sosai dan har ya fi sarki Gannami zalinci.

Sai dai ya na da matsalar k'wak'walwa an yi maganin, an yi maganin amma har yan zu be warke ba i dan haukan ya tashi kwana ya ke ya na ihu da doke -doke.

Duk macen da ya ka ma to sai ya yi ma ta fyad'e wannan fyad'en shi ne sanadin mutuwarta, idan kuwa ta rayu to ba za ta tab'a lafiya ba haka za ta yi ta jinya har ta mutu

Shiyasa iyayen 'ya'ya matan garin ba sosai su ke barin yaran su mata zuwa fada ba sabida b'acin rana.

Akwai wani mutum me su na lu'u yana da y'ay'a mata guda biyu lamma da hantsi kyawawa ne kaf garin ba ma su kyan lamma da hantsi tun da su ka fa ra tasawa ya ke b'oye su a gida ko tsakar gida baya ba ri su fito mahaifiyar su Rona ta na kulawa da su sosai komai a d'akin su su ke dan kar wa su su gan su, a gayawa sarki.

* * * *

Tsugune ta ke cikin dawakai ta na ta gyara wajen ko tsoro ba ta ji, sabida ta sa ba tun ta na k'arama Baban ta malam Ibrahim ya na zuwa da ita cikin dawakai Mahaifin ta shi ne sarkin dawakai

Yan zu Zeenat ke taya shi gyaran dawakan har wanka ta iya tayashi su yi wa doki.

"Baba wai shi wannan farin dokin ba a hawan shi ne, duk dawakan nan ya fi so k'arfi da lafiya"

"Hmmm Zeenatu kenan wannan dokin na yarima ZAID ne kwanan zai dawo daga k'asar ma su jajayen kunne "

"Allah Baba, dama ban tab'a ganin shi ba"

"Kin tab'a ganin sa mana sai dai ki ce ki na k'arama, yan zu shekaran sa bakwai be zo ganin gida ba ne"

"To Baba yan zu yau she zai zo?"

"Kin ci ka tambaya Zeenatu to ni ma bansaniba"

Haka su ke ta gyara dawakai su na hira daga ganin su akwai shak'uwa irin ta Uba da y'a.

Sarki Abdurrahman shi ne sarki me ci a yan zu shi ya bawa Malam Ibrahim sarautar sarkin dawakai,

Malam Ibrahim asalin su bayin sarki ne tun iyaye da kakan ni

Masarautar kumashi babbar masarau tace me cike da bayi da Al'adu da Malamai da sauran su.

Sarki Abdurrahma ya na da mata uku

Fulani Zahra'u itace uwargidan sarki ta na da y'a'ya uku Zaid shine babba, sai Safwan shekara uku ne tsakanin su da Zaid sai autar su Shukriyya akwai tazara sosai tsakanin Safwan da Shukriyya shekara goma ya bata.

Sai Hajiya Samira ita ce mata ta biyu a gurin sarki Abdurrahman y'ar sarkin Zazzau ce ta gaji sarauta gaba da baya yaran ta hud'u Firdausi,Shamsiyya,Saratu da kuma Khalil yaro d'an shekara bakwai duk burin ta ya na kan Khalil.

Sai Hajiya Hafsat ita ce mata ta uku a gurin sarki Abdurrahman ba ta tab'a haihuwa ba, ba ta da burin da ya wuce ita ma ta haifi magajin sarki, ita y'ar sarkin Sudan ce Sheik Yusuf Uwais

Ta na rik'on d'an Yayar ta, Lukman.

Bayan rasuwar Yayar ta ta ne ta nemi alfarmar sarki ya bar ta ta d'akko shi ta rik'e tun da ba ta tab'a haihuwa ba

Sarki Abdurrahman ya amince.

Sarki Abdurrahman ba shi da burin da ya wuce Zaid ya dawo ya mai da hankalin sa a harkar sarauta ya zauna ya ga yadda a ke gudanar da mulki, dan ya san duk Daren dad'ewa Zaid shi ne magajin sa tun da shi ne babban d'a awajen sa.

Waziri Alhaji Usman, shi ne amintaccen sarki Abdurrahman duk wa ni sirri na sarki to kuwa waziri ba bu Wanda be sa ni ba ya na da y'ay'a uku Hibbullah shine babba abokin Prince Zaid ne k'ud da k'ud yan zu haka su na can England ta re

Sai Bilkisu sai Aliyu Mahaifiyar su Amina matar waziri Usman.

Sai Jakadiya tsohuwa me yin iso ga kowa idan za'a ga sarki sai ta yi ma ka iso ko da kuwa Matan sa ne.

Zaman Gidan sarki Abdurrahman zama ne irin na kishin b'oye Zagon k'asa kowa ke wa abokiyar zaman ta.

Fulani Mahaifiya ga Zaid mace ce me ibada da tawakkali zuciyar ta a wanke ta ke ba ta nufin kowa da sharri.

Lafiya ta ke zaune da kowa

Ganin haka sai matan sarki biyu su ka had'e ma ta kai

Su ma kowacce a kwai k'ulli a zuciyar ta ta yadda d'aya ba za ta ga ne hakan ba dan kowa ta iya takun ta.

WANE NE PRINCE ZAID?

Zaid d'a ne na farko a wajen sarki Abdurrahman bin Abdul'azeez bin Zaidul'abideen

Asalin su larabawan Lebanon ne family ne me girma da su ka yad'u k'asa k'asa su ka dinga ka fa dauloli a haka a ka sa mu sarki Abdurrahman a k'asar Niger cikin garin Yemen.

Prince Zaid ya yi karatun sa ne a England, tun bayan da ya gama primary d'in shi a k'asar Niger a ka fi ta da shi abroad don ya cimma burin shi na za ma Gynecology Doctor (Likitan mata)

Yan zu ya kammala first degree d'in shi a harkar lafiya b'angaren matsalolin Mata, ya k'ware sosai a harkar shiyasa ma su ka rik'e shi a General hospital d'in su da ke England,

Zaid shaharen d'an POLO ne, ya san ta kan dawakai yan zu haka ya na buga wasan polo a America dan team d'in su su na ji da shi

Shiyasa har yan zu be sa mu ya zo Gida ba tsawon shekara bakwai kenan

Ya na so ya zo Gida Niger kafin ya koma ya yi masters d'in sa.

Duk wa ta harkar sarauta ba ta gaban sa ba shi da ra'ayin mulki ko kad'an

Ga magauta sun sa shi a gaba...,..,.....

Ki biya ki *karanta, hakkin* *mu ne*

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□ *MASARAUTARMU*

□□□□□□

Story & Writing By _R.Hussain_

&

Noory

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

Wannan littafin *na kud'i ne*

Normal group *N300*

VIP N500

Ki *biya ki* *karanta cikin* *aminci*

2414444137

Zenith *bank*

Rahinat Hussain

Ki tura shedar biya ta wannan number 08107916039

Idan kuma recharge card ne MTN ta wannan numbers 08107916039 kuma 08145498489. Bamason VTU

.....Sarki Gannami ya ce" Haba Hazid, kaf matan garin nan na Duhuwa ba wadda ba ta zuwa fada domin yin gaisuwa, ko sabuwar haihuwa ne kuwa to kuwa in ba aljana ka ke ga ni ba to idanun ka ne ke nu na ma k'arya, dan budurwar cikin madubin tsafin ka ba mutum ba ce"

"Hannun sa ya d'ora akan sa alamar rantsuwa" Na rantse da tsafin kaka na Lausir ba aljana ba ce, mutum ce ku ma a cikin garin Duhuwa ta ke"

"To Hazid na ji je ka zan sa a ne mo maka ita ko ina ta ke a duniyan nan"

Fita Hazid ya yi da ga d'akin sarkin,duk kan bayi matan da ke gurin sun gudu dan inhar ki ka yi wa Hazid to su nan ki gawa, fyad'e ze mi ki ya kuma kashe ki in dai a cikin gidan sarki, ki ke aiki ba'a Sanin Hazid ku ma ki cigaba da rayuwa a gidan su.

Shiyasa Matanen gari 'yan mata ba su had'a hanya da Hazid

Lamma da hantsi ne su ke hira a cikin d'akin su " Hantsi ni kuwa ina so inje Gidan sarki Gannami, tun da na ke ban tab'a ta ka k'asar waje ba, ba re Gidan sarki ke ma ki na so ki je?

Cikin sanyin halinta ta na wasa da hannun ta ta d'ago kan ta ta ce "A'a"

Ta na k'ara girgiza kanta

"I dan ki ka fita mutuwa za ki yi Rona ta gayama na ai"

"To shikenan Sai mu yi ta zama cikin Gidan ga har mu mutun"

"Eh anan za mu yi ta zama, Lu'u ma ya gayama na"

" To na rantse da K'AININA sai na fi ta watarana"

Kwanciya ta yi ta k'yale hantsi

Lamma ita ce yayar Hantsi ta girme ta da shekara d'aya, lamma ba ta da dad'in kai kamar Hantsi duk da Hantsi ta fi lamma kyau ne sa ba ku sa ba, duk da lamma ma ta na da na ta kyan,

Rona Mahaifiyar su ce ta shigo ka wo mu su abinci

Wani irin tuwo ne bak'i k'irin da wa ta miya kamar jini

Ganin ya na yin y'a'yan na ta ne tasan

Sun yi fad'a

"Lamma ta shi ki gayamin me ya had'a ku so ku ke K'ainina ya la'ance ku ku ke fad'a?"

Sanin halin Hantsi ba za ta yi magana ba ya sa Rona tambayar Lamma duk da Hantsin ta na zaune

"Rona nagaji da zama a cikin wanga Gida na rantse da kakan Lu'u watarana sai na fita"

" Lamma!!!!Rona ta kira ta cikin ta shin hankali ki na so sarki Gannami ya aure ki ko kuma d'an sa ya kashe ki?"

"Rona ganin su na ke so na yi"

Tunani Mahaifiyar su Rona ta ke na sa mun mafita ga shi ba ta son rasa y'ar ta

"Zan kai ki fada wa ni lokaci zan shafa mi ki shuni zan go ga mi ki ruwan rogo fatar ki ta ya mushe

Za ki ga sarki Gannami da Hazid cikin siffar tsohuwa Lamma

Murna ce ta kama Lamma rawa ta ke ta yi alamar farinciki kenan

Hantsi kallon su kawai ta ke dan ita ba ta damu da rayuwar da ta ke a haka ba

Hazid ne gaban madubin tsafin sa kallon Surar kyakyawar budurwar da ta rufe fuskar ta da farin k'yalle ya ke son ta ya ke kamar ya mutu ga shi ba damar tab'ata

Ihu ya kwalla haukan sa ya tashi

nan da nan a ka d'ak ko k'atuwar sark'a a ka d'aure shi

Ba za a sa ke shi ba har sai ya dawo hankalin sa

"Na rantse da K'ainina ba zan ta b'a sab'a maganar Lu'u da Rona ba, ke da za ki je Lamma ki ta fi idan a ka kashe ki shikenan"

"Za'a can za min kama ai ni sai na ga Sarki Gannami da d'an sa Hazid"

Shiru ne ya biyo ba ya

Jikin Lamma ya yi sanyi haka dai su ka shirya su na hira har bacci ya d'au ke su

Ba sa iya share junan su dan su na k'aunar junan su sosai

Haukan Hazid ya ta shi sosai cikin Daren nan ba wanda ya yi bacci a fada

Mahaifiyar sa Shiwu sai buga kan ta ta ke a bango ta na ihu

Sarki Gannami ma sai kai kawo ya ke a fadar

"Wanne irin ciwo ne wannan kamar ni sarkin garin Duhuwa a ce tsafin ya ka sa warkar da d'a na

Boka 'Dundumi ne ya bayyana a fadar

Shi ya san mutanen da za su zo ne kad' ai su ke da maganin ciwon Hazid

Cikin sauri shiwu ta je gaban Boka 'Dandumi " ya shugaban bokayen duniya ka warkar min da d'ana, ya na jiwa kan sa ciwo" kuka ta ke sosai cikin fitar hayyaci

Sarki Gannami ne ya rungume ta ya na rarrashin ta,Ubo ce ta koma d'akin ta na jin dad'in wannan ciwo da ya sa mi Hazid

Boka ne yace....,.

* * * *

"Zeenat in go abincin nan ki kai wa Baban ki ya na cikin dawakai yau kin k'i rakiya ai"

" To" d'aukar kwanon abincin ta yi ta ta fi kai ma sa

"Assalamu Alaikum sannu da aiki Baba na"

"Yawwa Zeenatu"

Wanka ya ke wa dawakan da aka siyo wa prince Zaid

"Baba wannan dawakan sarki me?"

"A'a Zeenatu na yarima Zaidu ne, zai dawo daga

 karatu"

Cikin farin ciki da d'aukin za ta ga yarima babba dan shekara bakwai ke nan be zo k'asar ba

"Au ho!! Ashe shiyasa na ga ana ta gyara ko ina a na ta k'ara shirya wancen part d'in

Ashe shi ne zai dawo"

"Eh Zeenatu"

Prince Safwan shi ne k'anin Prince Zaid,Safwan d'an nanaye ne duk wa ni club club na big guys Safwan ya San shi ga shi da 'yan mata kala -kala duk wa ni d'an manya ma ra ji to d'an team d'in su Safwan be

Prince safwan sai murna ya ke d'an Uwansa Prince Zaid ze iso k'asar ta su ta Niger domin akwai kyakkyawar mu'amala tsakanin su sai dai zuwan Prince Zaid zai dena wa su abubuwan na rashin ji.

Fulani Samira matar sarki Abdurrahman ta biyu ba ta da burin da ya wuce sarautar Kumashi ta dawo hannun ta, sai dai d'an da ta ke bu ri a kan sa Khalil k'aramin yaro ne, ga manya biyu a gaba sa Prince Zaid da Prince Safwan yan zu k'udurin ta shi ne ta kau da su a doron duniya, tun da ta ji Zaid ze dawo ta d'aukin alwashin ajalin sa ne ya dawo da shi duk yadda za'ayi sai ya mutu a wannan zuwan ba za ta ba ri ya dad'e ba.....

Shin su waye za su bak'unci Masarautar DUHUWA

waye zai warkar da Hazid ?

Wace a cikin madubin tsafin Hazid?

Shin Prince Zaid zai dawo kuwa ko Fulani Samira za ta yi nasarar kawar da su?

Ki biya ki karanta hakkin ki □□

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□ *MASARAUTAR MU*

□□□□□□□

Story & Writing By _R.Hussain_

&

Noory

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

Wannan littafin *na kud'i ne*

Normal group *N300*

VIP N500

Ki biya ki *karanta cikin* *aminci*

2414444137

Zenith *bank*

Rahinat Hussain

Ki tura shedar biya ta wannan number 08107916039

Idan kuma recharge card ne MTN ta wannan numbers 08107916039 kuma 08145498489. Bamason VTUƍ

Protection comes only from Almighty Allah,whoever Allah guides, He is rightly guided.May Almighty Allah continue to guide and protect you and your family. May Allah never let your heart be distributed by the trials of life, ease your ways, accept your ibadah,bless yor end and grant you and your family jannatul firdaous, Aameen □□□□. *JUMA'AT MUBARAK*

Ɓage

.....Jakadiya ita ce masaniya a cikin Gidan sarki Abdurrahman duk wani tuggu da makirci idan ya biyo ta hannun Jakadiya to kuwa inshaallah komai zai ta fi successful, dan Fulani ta yadda da ita fi ye da tunanin me tunani.

Lukman d'a ne ga Fulani Hafsat, don y'ar yayar ta ne ta ke rik'o, kasan ce war su larabawan Sudan shiyasa Lukman ma ya ke da kyau sai ya saje da y'an Gidan sarki Abdurrahman

Tunda asalin su Larabawan Lebanon ne.

Lukman ya na son sha'anin sarautar bak'ak'en fata shiyasa da Hafsat ta ce ya dawo gurin ta da zama ba mu su ya amince.

Fulani Hafsat ta na da manufar hakan a ranta, Lukman ya shi ga jikin Prince Zaid sosai da sosai, duk wa ni abu na Prince Zaid Lukman ya sa ni, dai dai da halin da zuciyar sa ta ke ciki,Lukman tsaf ya ke karanta a kan fuskar sa.

Hibbullah ya tsani Lukman sabida ya na ga ne waye shi a matsayin sa na barrister Hibbullah Usman Waziri,Hibbullah ba ya sakin jiki sosai da Prince Zaid a Niger sabida mutum ne me taka tsan- tsan da kowa.

"Gafara toron giwa,lafiya dai sarkin Musulinci,sarki me adalci gaba salamun ba ya salamun" Jakadiya ke ta zabga kirari ga Sarki Abdurrahman.

"Angaishe ki Jakadiya,sarki ya amsa" Inji Sallama

"Yauwa godiya na ke sallama, Ran ka dad'e Fulani babba ke ne man a yi ma ta iso"

Sarki ne cikin Alka'bbar k'asaita da golden d'in rawanin sa da hannu ya nu na alamar ta jira shi a turakar sa.

"An yi ma ta Jakadiya ta jira shi, a ciki an gaishe ki Jakadiya"

A kishingid'e ta ke a kan lallausan Capet d'in d'akin sarkin ta d'ora gwiwar ta a kan tum -tum Apple ta ke ci, so ta ke ta ji yaushe gudan jinin ta yarima Zaid zai shigo Yemen d'in.

Motsin shigowar sa ne ya sa Fulani ta shi ta tari mijin na su, wannan hali na Zahra'u ya na k'ara wa sarki Abdurrahman k'aunar matar ta shi, ta na ma sa biyayya fi ye da sauran matan sa, ta na manta wa ita ma me matsayi ce, baiwa sosai ta ke zama a gaban mijin na ta.

Girmama wa da hidim ta wa kawai ta sa ni a gaban sarkin.

"Barka da shigo wa ran ka ya dad'e"

Murmushi ya yi ya k'ara sa kusa da Fulani hannun ta ya kama su ka zauna a Royal bed d'in sa ta re.

"Ina jin ki Fulani me ki ke so"

"Hmm ba'abin da nakeso illah sanin yau she Zaid ze da wo, dan in tanadar ma sa favorite meal d'in sa"

"Murmushi me martaba ya yi " Fulani kenan ke ko irin kunyar nan ta y'ay'an fa ri ba ki yi akan Zaid ko"

"Haba dai zaujee ina yi mana, kawai dai so na ke ya ji dad'i,shi ma ya dawo ya tarar da karb'a ta musamman a wajen iyayen sa ko da ya kema na san halin Magaji yan zu ya iya ce min " ammi I'm full na ci shawarma a cikin flight just keep it may be later I will eat"

Dariya su ka sa ita da sarki Abdurrahman, dan yadda ta ke kwatan ta reaction d'in Prince Zaid kamar shi d'in ne ya ke yi.

"Kun fi ku sa ai ke da d'an na ki" motsin tab'a k'ofa su kaji, kallon k'ofar turakar ta sa su ka yi cikin mamakin wa ye a wajen.

Har da ya wuce corridor d'in sa ya wuce falon sa ya shigo har jikin k'ofar turakar sa, ku ma Jakadiya ta san ya na tare da Fulani.

"Ba ri na koma ranka ya dad'e"

"Ba za ki tsaya ki yi aikin lada ba?"

Murmushi ta yi ma sa" ai ba ni ke da kai ba yan zun ma nasan sai an zarge ni, ka sa hak'uri na yi shiyasa na zo jin yau she zai dawon"

"To Fulani sauka lafiya".

Bud'e k'ofar ta yi ta fito, amma ba ta ga kowa ba har Jakadiya ba ta bak'in corridorn

Mamaki ne ya ka ma Fulani sanin Jakadiya ba ta nisa da nan gurin,amma yan zu ba ta ganta ba.

Kamar da ga sama Jakadiya ta shigo"tuba na ke ranki ya dade na dan za ga ne rankin ya dad'e a gafar ce ni"

Kallon ta kawai Fulani ta yi amma ba ta ce komai ba, giftawar inuwar Mutum ta ga ni an wu ce da sauri, baiwar ta hidaya ce ta ta so ta ta ke ma ta baya ta na gyara ma ta alka'bba su ka koma part d'in ta.

"Lukman ka san dai da kai na dogara a cikin Gidan nan, yan zu idan me martaba ya fad'i ya mutu to kuwa daga ni har kai barin masarautar nan za muyi,tun da ni ban tab'a haihuwa ba kai kuma ba d'an sa ba ne, me ne ne mafita,dan tun yan zu za mu samawa kan mu"

"Hmmm Aunty ke nan,duk kin bi kin damu da wannan sarautar kin manta da MASARAUTAR MU ta Sudan ne, Prince Zaid d'in ma da ki ke magana akan sa ba son sarautar ya ke ba, ya fi gane wa Polon sa.

" kai dallah yi min shiru,ni da ma ban d'akko ka ba"

Murmushin mugun ta Lukman ya yi,ya na shafa gemun sa.

"Ke sarautar kad'ai ki ke so ni kuma gaba d'aya ahalin Gidan sarki Abdurrahman na tsana,ina jin damuwa da bak'in cikin na bud'e idona na ga P.....

* * * *

Prince Zaid zaune a gefen beach ya na tunanin futsara irin ta yahudawa da nasara ga su dai kamar mutane amma ba su ba ne.

" Prince yadai?"

Hibbullah ya zo kusa da shi rik'e da ice cream biyu a hannun sa mik'awa Prince ya yi ya zauna dan jin ya ne.

"Friend ba komai, kawai tunanin rayuwar nan na ke yi"

"Kai dai fad'i gaskiya ko ka ga wacce ta yi ma me?"

"Mtswwww Allah ya ki ya ye,kai mata su ka dama banza kawai"

"Hahhhh ni ai aure na ce zan yi ba wani abu ba ku ma kasan sunnar Manzon Allah(SAW) ne ko"

Idan ka ga ma ka tawo"

"Hahh Allah ya nu na min ranar da wata baby za ta yi wuff da zuciyar ka Prince Zaid"

"Kan ka akeji".

Sera ce ta tawo da gudu daga ita sai pant da wata damammiyar za ta rungume Prince Zaid ya yi saurin matsawa ya na ma ta kallon mahaukaciya k'azama.

" are you mad,eyeeh nonsense you're foolish i told you I don't love you, I hate you with all my heart, idiot mtswww.

Hawaye ne ke sharara a idon baturiyar kallon sa ta ke kamar za ta cinye shi, son sa ta ke fi ye da k'ima.

"I'm so sorry serah

Please"

Hibbullah ke ta rarrashin ta, dan tausayi duk wacce ta ce tanason Prince Zaid ya ke shi.

Haka kowa ya kama hanyar gida zuciya ba dad'i.

"Oh Allah!! Zeenatu ba za ki fito haka ba ne?"

Zeenat ce ta fito fuskar ta kamar.....

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□ *MASARAUTARMU*

□□□□□□

Story & Writing By _R.Hussain_

&

Noory

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

Wannan littafin *na kud'i ne*

Normal group *N300*

VIP N500

Ki *biya* *ki* *karanta cikin* *aminci*

2414444137

Zenith *bank*

Rahinat Hussain

Ki tura shedar biya ta wannan number 08107916039

Idan kuma recharge card ne MTN ta wannan numbers 08107916039 kuma 08145498489. Bamason VTU

..... Sudees ke ta hada - hadan had'a 'yan JIHAD DA'AWA FOUNDATION k'ungiya ce da ta shahara wajen d'aukaka Kalmar Allah, su kan je cikin garuruwan Maguzawa,pagans, dasauransu. sudees aboki ne ga Prince Zaid sun had'u ne a Saudia, sun je umarah, asalin sudees d'an Nigeria ne wannan had'uwan sai Allah ya sa abokar ta su ta d'ore dan har yan zu kowa ya na ziyar tar abokin sa, idan sun sa mi dama.

Sudees d'ane ga sheik Umar gadon k'aya ya yi karatun sa ne a jami'atul Madina in da ya karanci Ulumul tafseer bayan ya dawo ne ya ka fa JIHAD DA'AWA FOUNDATION matashin saurayi ne Wanda be haura shekara 30 ba, Allah ya ba shi baiwar ilimi both side Arabic da Boko

Idan ya juya harshe sai ka d'auka ba d'an Nigeria ba ne kyakkyawa ne dan tamkar balarabe haka ya ke, sun musuluntar da mutane da yawa a sassa daban _daban.

Sudees ne zau ne a cikin masallaci ya na tafseer dan in dai ya na k'asar nan cikin garin Kano to kuwa baya zama haka dole sai mahaifinsa ya sa shi Tafseer dan Allah ya hore ma sa hikima da balaga

Gama tafseer d'in sa kenan sun yi sallar Isha'i Hamza ya kawo ma sa wayar sa

"Ya sheik Tun d'azu Prince Zaid Niger ya ke kiran ka"

Murmushin da ya za me ma sa jiki ya yi dan ko da yaushe ba ka raba shi da shi a fuskar sa (smile is sunnah) " mashaallah"

Karb'ar wayar ya yi ya k'ira shi

"Wa'alekumus'salam warahmatullah the Prince of princes"

Daga can cikin filin su Wanda su ke buga Polo prince Zaid ya ke waya

" Malamai magada Annabawa fatan komai lafiya?"

"Alhamdulillahi, ya England ya wasa ya karatu?"

"Hmmm Haba ya sheik ai sai a d'auka wasa na ke Polo fa business ne dan team sai ya siye ka a price me kyau fa"

" kai Prince ni duk

Wannan abubuwan ba sa gaba na, ka dawo kawai ka temakawa al'umma ga marasa lafiya nan da yawa ma su buk'atar professional doctors irin ka k'aki'i dawowa K'asar ba re mu ma Nigeria mu sa ran za ka kawo ziyara"

Hira su ka yi cikin nishad'i da ga ganin su akwai kyakkyawar mu'amalah a tsakanin su ban kwana su ka yi wa juna, Sudees ya shiga cikin gida.

Umma ce zaune a falo ga su Yusra da Amal su na ta Homework d'in su

Harun kuma ya na d'akin sa ya na chat da budurwar shi Ameera su ne kad'ai su ka rage a gidan.

Amina ita ce ta ke bin Sudees ta yi aure yan zu yaran ta uku, mata biyu namiji d'aya sai zuhura itama ta yi aure yaran ta biyu duk maza.

Sudees ne akeso shima ya yi auren, amma ya k'i mai da hankali, Matan ma tsoron su ya ke ji, dan y'ay'an manya da y'ay'an sarakuna su masifar son sa dan sudees k'arshe ne ga kyau na d'aukar hankali, ga kud'i ga ilimi amma ba sa gaban sa.

"Assalamu Alaikum Ummi na"

"Wa'alekumus'salam yaro (d'an fari ne umma yaro ta ke ce masa)

" Na'am, nagaji sosai Ummi na"

"Sannu ai kana k'okari Allah ya ba ka lada ba ri a kawo ma ka abincin"

"A'a Ummi na fresh milk ma is okay"

"Aikin kenan shiyasa Haruna ma ya fi ka auki ai"

"Hmmm Ummi na"

Daga haka be k'ara cewa komai ba dan magana wuya ta ke ma sa, sai Umma da Sheik Umar Mahaifin sa sai kuma a gurin Da'awa.

* * * *

Boka 'Dundumi ne ya gyara sandar sa ta tsafi zai yi magana kenan, sarki ya dakatar ta shi "Me ka zo yi ba ka da wani amfani tun da ka ka sa warkar min da d'ana "

Boka 'Dundumi be fa sa ba ya ce" ya shugaba na akwai abin da zai warkar da yarima amma ya na da wahala ka amince"

"Me ne shi, gayamin komai wahalar sa zan yi"

Jimmm Boka 'Dundumi ya yi sannan ya ce

"Akwai wa su mutane da za su zo cikin garin nan.....

"Banason jin zancen nan ta shi ka ta fi"

'Bat boka ya b'ace

Haka garin Duhuwa ya kwana cikin tashin hankali kuma ba mafita

Tunda boka 'Dundumi ya koma halwar tsafin sa buncike ya ke ta yi dan samun wa ta hanyar da zai ba wa yarima lafiya, amma hanya d'aya ce zuwan wannan mutanen da za su yak'e su, su ka fa Sabon addini shi ne kad'ai zai sa Hazid ya sa mu lafiya.

Mamakin k'arfin mutanen ya ke, kuma yaushe zasu zo wanne irin k'arfi ne da su har da za su yi galaba akan su

"Kaiiii!!!!!!!Ina ba zan tab'a ba ri hakan ta faru ba buri na in zama sarkin Duniya ba sarkin Duhuwa kad'ai ba muddin na ba ri wad'an nan yaran su ka so, to Ku wa tabbas sai abun nan ya fa ru, Sabon addini da ku ma ka fa ta su masarautar to MASARAUTAR MU fa?"

hahhhahhhh dole in dakatar da zuwan su dole ne"

Sai da rana ta fito sosai Hazid ya dawo hankalin sa ganin sa d'aure da sarka ya sa ran sa k'ara b'aci, Mahaifiyar sa Shuwi ita ce ta zo duba shi, ganin ya dawo hankalin sa ya sa ta fad'a cikin sa ta na kuka "d'a na maigirma Gannami ya k'i ne ma ma ka magani boka ya ka sa yi ma ka komai"

Kuka Shiwu ta ke ta na jin bak'in ciki a ranta

"Shiwu Ki dena kuka na rantse da kai na zan yi maganin Boka 'Dundumi na san ya na sa ne, ya k'i ba in lafiya dan na San ba'abin da ya fi k'arfin sa"

Kwance shi ta sa akayi kwarya ta sa a kai ma sa bayi domin ya yi wanka da ruwan sihiri wan da ko da yaushe da shi ya ke wanka.

Tuno budurwar sa ta madubi ya yi "Shiwu ba ri ki ga mata ta ita zan aura dan sai na ne mo ta duk in da ta ke a duniya ko da zan ra sa komai na wa"

Sanin ya na da matsalar k'wak'walwa ya sa Shiwu ba ta mu sa ba, duk abin da ya ce bin sa ta ke da hakane

Ubo kuwa ganin Shiwu ta dad'e ba ta fi to ba, ya sa ita ma zuwa d'akin dan ganin mahaukaci Hazid

"Mai girma Hazid ka da wo K'ainani ya du ba ka ya sa ka warke"

"Me ki ka zo yi, nasan abin da ki ke shukawa Ubo kallon ki kawai na ke yi"

Sanin da ta yi Hazid ya na da tsafi shiyasa ba ta mu sa ba, dan da ya so zai iya kashe ta kuma ba abinda za'ayi akan hakan.

Fi ta ta yi ta na hak'ura da cikar burin ta dan ta san Hazid shu'umi ne, cutar da ya ke da ita ce kawai ta gagare shi ta kuma gagari duk wa ni tsafi na su da k'alau ya ke sai ya fi ha k'a zalunci "na rantse da K'ainani sai na ne no mata ta a duniyar nan ina jin k'anshin ta ku sa da ni, muddin ba ta mi k'a manta ga re ni ba har na wahala a Neman ta sai na ma ta hukunci ma fi tsanani a MASARAUTAR MU.....

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□ *MASARAUTAR MU*

□□□□□□

Story & Writing By _R.Hussain_

&

Noory

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

Wannan littafin *na kud'i ne*

Normal group *N300*

VIP N500

Ki biya ki *karanta cikin* *aminci*

2414444137

Zenith *bank*

Rahinat Hussain

Ki tura shedar biya ta wannan number 08107916039

Idan kuma recharge card ne MTN ta wannan numbers 08107916039 kuma 08145498489. Bamason VTUǫ

MASARAUTAR DUHUWA.

Sarki Gannami ne zau ne a kujerar azurfa ya sha kwalkin sa na fatar zaki jikin sa sanye da mayafin fatar damisa, kansa d'auke da hular gashin dawisu an yi ma sa a do da hauren giwa dogwaye guda biyu, gefen sa Hazid ne zau ne da irin shigar Mahaifin sa, sai dai shi kan sa ba hauren giwa.

Tsaye ya ta shi ya na kallon mutanen da su ke cikin fadar ta sa, kowa ya na tsaye sahu - sahu gaisuwa su ke ga sarki Gannami da Hazid bud'e hannu wan su, su ke kamar za su ta shi sama.

Sai da sarki Gannami ya zauna sannan kowa ya zau na.

"Ya ku mutanen fada sarki ya ce asanar da kowa da kowa wannan shekarar da mata da maza yara da manya ma su lafiya da marasa lafiya dole ne a fito a so wajen bikin shekara"

Hankalin samarin fadan ne ya tashi, kowa ba ya son a zab'e shi a matsayin hadaya ga dodon shafi K'ainani.

"Wayyo Bisi mun shiga uku,K'ainani ya a gaje mu, ni banson wannan al'ada ta Duhuwa, ba na son kwanciya da y'ar kowa,ina ji a jiki na akwai gagarimin Abu da zai faru a nan gaba, ba na so na mutu banga lokacin nan ba".

Zama Timi ya gyara sannan ya ce"Tun kafin wannan lokacin na ba ka shawara ka samu wata ka yi ka huta da wannan fargaban amma ka k'i, kasan kuwa yadda abun nan ya ke na rantse ma ka da K'ainani akwai dad'i"

"Mtswww bazan ta b'a aikata wannan ba Timi"

"To kuwa a wannan shekarar za ka zama hadaya tabbas"

Haka zaman fada ya tashi ko wa na tunanin y'ay'an wa za'a ba yar a matsayin hadaya.

Lamma ce ta ke ta kumbure - kumbure an ce za'a je da ita fada, amma shi ne Rona da lu'u su ka ta fi su ka barsu kamar kullum.

"Hantsi kin ga gari ba kowa sai mu kad'ai ki zo mu je mu ma"

Cikin yanayin ta kamar kullum ta girgiza kan ta, ta ci gaba da shirunta.

Bisi ne ya ke saran itace,guri ya nema ya zauna,duk tsoro da fargaba ya ke ji,kar ya za ma hadaya,hanyar da zai kub'utar da kan ya ke nema, amma ya rasa.

Timi ne ya tab'ashi"Bisi tunanin me ka ke yi ne haka?"

"Mafita kawai na ke nema Timi, bazan iya aikata wannan abun ba na rasa ya zanyi.

" kwantar da hankalin ka ni zan sa mi wata, in aikata sai ka zo wajen ni kuma sai na gudu, idan mutane su ka zo shikenan ka zama tsarkakke"

Ajiyar zuciya Bisi ya yi "godiya na ke Timi ka temake ni kuwa,K'ainani ya temake ka"

Da haka su ka cigaba da faskaren itacen su.

"Rona kin yi wa Lamma k'arya,kuma kin san ko sarki Gannami ba yason k'arya ba re K'ainina"

"Hantsi ban samo tsunin da zan mata aiki ba ne, amma zuwa na gaba da ita zan je kinji y'ata?"

"Kai ta d'aga kawai ta kalli Lamma wacce har yan zu fushin ta ke yi.

"Lamma za'aje da ke kinji, K'ainani ya sa ki gansu ki zo ki ba ni labari"

Sai lokacin Lamma ta yi dariya.

Rona ce ta ke ta had'a mu su abinci, mak'ociyar ta lantan ce ta shigo cikin rashin sa ni Lamma ta fito ido su ka had'a da lantan,

Fargaba ce ta ka ma Rona.

"Rona wannan ce y'ar da ki ka haifa ki ka ce sun mutu ko?"

"A'a Lantan ki gafarce ni K'ainani na ke son ba wa hadaya idan su ka girma, ko na yi albarka"

Ji su ka yi ammake Lantan ya fad'i a sume kan ta ya fashe.

Ganin kyakyawan Namiji su ka yi tsaye a cikin gidan murmushi kwance akan fuskar sa.

Sudees ke ba wa samarin unguwar fatawa,akan wa ta tambaya da aka rubuto masa, cikin k'warewa da fasahar harshe ya ke amsa wa.

Samari da dattijai kowa koyi ya ke da Sudees an sha ba shi kyautar mata, ya na yin fuska ya k'i amsawa,dan idan ka fad'a sai ya yi shiru ya sunkuyar da kan sa.to no answer.

Jama'a da dama su na tunanin aljana ce ta aure shi, ko kuma ba shi da lafiya.

Yusra ce ta fito daga d'akin umma "Wallahi umma Amal ta shiga d'akin yaya Sudees sai b'ata ma sa littafai ta ke"

"Kira min ita,kar ya zo ya da ke ta,ni ba ruwa na"

Kamar anjefo Sudees"Assalamu alaikum"

Ganin yanayin Yusra ya sa shi tambayar lafiya?

"Wallahi yaya ni ba ruwana Amal ce"

"Me ta yi?

" kimin shiru"

"Ka je d'akin ka zaka ga abin da ta ke yi"

Da sauri ya nufi d'akin na sa tsaf ya gan shi kuma ba Amal d'in a ciki.

A can kuwa Sultana ce ta ba wa Amal congealer ta d'akko ma ta picture d'in Sudees, Son sa ta ke jini da tsoka.

Shi kuma ya k'i ba ta dama, cousin d'in sa ce dan y'ar k'anwar Sheik Usman Gadon k'aya ce.

Harun ne a compound d'in gidan ya na zaune a kan d'aya daga cikin motocin Gidan na su, chatting ya ke yi da abokan sa,

"Assalamu Alaikum"

Hannu Hamza ya mik'a ma sa su ka yi musabaha

"Wa'alekumus'salam malam Hamza"

"Ya mutumin ya na ciki kuwa?"

"Eh yan zu ya shiga, ka shiga cikin"

"Okay nagode"

Wuce wa cikin Gidan ya yi dan samun Sudees da maganar Visar da za su yi don zuwa k'asar Morocco da'awa.

Yana cikin kallo ya ga yadda wani yan ki su ke rayuwa,kamar dabbobi, tun daga lokacin ya d'auki niyyar zuwa garin domin kira zuwa ga addinin musulci.

'Yan kungiyar JIHAD DA'AWA FOUNDATION ne wasu za su wakilci wasu su je Moroccan wa su kuma sai su hak'ura,Hamza da su Yusuf,Abdullahi,khalid, da su za'ayi tafiyar, yan zu komai ya kammala shi ne yazo nu na wa Sudees Visa d'in

"Lukman me ye shirin ka game da dawowar Prince Zaid d'in nan ne????????

Waye ya zo cikin Gidan su Lamma?

Shin Lantan kuwa ta mutu ko a'a?

Wai Sudees wa ce yarinya za ka so ne?

Ya za ta kasance da Lamma idan ta je ganin sarki Gannami da Hazid???

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

MASARAUTAR MU

□□□□□□

Story & Writing By _R.Hussain_

&

Noory

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

Wannan littafin *na kud'i ne*

Normal group *N300*

VIP N500

Ki biya ki *karanta cikin* *aminci*

2414444137

Zenith *bank*

Rahinat Hussain

Ki tura shedar biya ta wannan number 08107916039

Idan kuma recharge card ne MTN ta wannan numbers 08107916039 kuma 08145498489. Bamason VTU♀

....."Gaskiya Prince ba ka kyautawa haba dan Allah kai ta wulak'anta mata akan su na son ka,mtswww"

"Hibbullah ni nace su so ni, ko kuwa narasa wacce zan so sai Christan Allah ya kiyaye kai ni malama zan aura ingayama ka ma"

"To naji, but Sera me ta yi maka yan zu a cikin mutane ka wulak'anta ta fa, haba Prince Zaid kasan dai haramun ne"

"Okay it means in bar ta tayi hugging d'ina ko, mutunci na ya zube a idon duniya ko, kana sa ne da kallon da ake mana a can Masarautar mu ko?"

"Ai Allah ya na ga ni, duk zaman da mu ka yi anan ba ma fasik'anci, kuma Allah shi ne shahidi, zai sa ka mana"

K'arasa maganar ya yi cikin kulewa da tuno zargin da su Hafsat da Samira matan sarki Abdurrahman su ke musu.

"Hmmm to man da zarar na bari ta rungume ni Wallah ko kaffara babu sai hoton ya je har gaban memartaba,

Duk abin da zai sa a zarge ni ko a ka mani da lefi ina gudun sa"

"Hakane Prince I understanding you".

Wanka prince Zaid ya shiga shi kuma Hibbullah system d'in sa ya kunna dan ganin me ke going a duniya.

Prince Zaid tun da ya shiga toilet d'in,ruwa kawai ya sakar wa kan sa,zuciyar sa cike da damuwa, me na yi wa mutane ne su ke son ganin aibu na more especially y'an k'asa ta?

Su kuma mata duk kan su jarababbu ne, duk in da nashiga sai sun bi ni,may be ma had'a baki ake yi da su dan a cutar da ni,kuma inshaallah duk me son ganin baya na sai dai ni naga bayan sa.

Da tunani kala - kala ya gama wankan.

Fulani Hafsat ce matar sarki Abdurrahman Abdul'azeez ta biyu ke yi wa princess Firdausi fad'a.

"Ke ko zuciya ba ki da ita,kina kallon matar nan ba k'aunar mu ta ke a cikin Gidan nan ba, amma ke da ya ke natacciya ce kullum kina part d'in ta, to Dan Uban ki me ki ka je yi part d'in ta?

Shiru Firdaus ta yi,hawaye kawai ta ke sharewa, ta rasa me Fulani babba ta yi wa maman su,ta ke ma ta wannan k'iyayyar ita dai ba ta ga wa ni abu na cutar wa da Fulani ko Safwan su ke mu su ba, Prince Zaid kuwa ba ma a k'asar ya ke zama ba.

"Ina magana kin yi min shiru ko?"

"Wallahi umma ba wani abu na je yi ba,kawai gaishe da....bi ge mata ba ki Fulani Hafsat ta yi" idan na k'ara jin an ce min kin je part d'in ta ni da ke ne, mara zuciya wacce ba ta kishin Uwar ta, ta shi ki ba ni guri"

Shamcy ce tace "Allah Umma kamar ba ke ki ka haifi Princess ba, irin halin Fulani babba ne da ita"

Saratu na jin su kasan ce warta k'ara a cikin su, ba ta sanin wai kishi a Ke yi da su Shukrah dan ita sa'ar Shukrah ce, Ku ma ko an hanata zuwa part d'in sai ta je ba ruwan ta da rayuwar su.

"Yallab'ai ni kam su Hibbullah shiru har yan zu,yau she za su girma su de na mana k'arya ne?"

Murmushi waziri Usman ya yi "ba ri in kira mi ki shi sai ki ji da ga bakin sa"

Wayar sa ya d'akko ya shiga kiran his son d'in na su, sai da Ringing d'in ya yan ke,sannan Hibbullah ya bi yo(wanna shi ne k'a'idar su ba sa tab'a d'aukar kiran iyayen su)

Video call ya k'ira su

"Assalamu Alaikum"

Farin ciki ne ya cika zukatan Amina da waziri ganin ingarman d'an na su cikin lafiya da kwanciyar hankali,ya k'ara kyau da girma kamar irin black American nan, kwantaccen sumar sa sai shining ta ke ga ta har wajen kunnen sa,Beard d'in sa a kwance luf - luf bak'i mai shining, murmushi ya ke sakar wa mahaifan na sa.

"My son yakake" cikin zumud'i Hajiya Amina ta ce.

"I miss you my patent, ina lafiya umma na,ya kowa da kowa?"

"Lafiya lau, ina Zaidul'abideen d'in?"

"Prince ga umma"

Ta so wa ya yi ya dawo kusa da Prince d'in dan girma ma wa ga Zaid d'in.

"Assalamu Alaikum"

Cikin jindad'in yan da su Prince d'in su ke rayuwa lafiya lau, ba tare da shashancin samarin zamani ba ta amsa.

"Wa'alekumussalam yarima"

"Umma Ku na lafiya, da fatan komai ya na lafiya normal"

"Alhamdulillah yarima,ya turawa,sun dai hanaku dawowa mahaifar ko ko?"

Murmushi ya yi yace "A'a kam muna nan ta fe inshaallah"

Waziri ne ya karb'i wayar su ka gaisa cikin girmama wa, sannan su ka yi sallama.

Prince ka hak'ura da wasan world's cup d'in nan, in ya so next year sai, a yi da mu"

Kallon ba ka da hankali ya yi ma sa"Amma Hibbu ba ka da kai, kasan kuwa burin da ba ci na gani na buga world's cup d'in nan, to idan ka ga ban tsaya na yi ba ko, sai dai ikon Allah"

K'arasa shirya wa ya yi ya fice.

"Jakadiya kin san komai na Gidan nan, kuma nasan kin dad'e da maimartaba ko?"

"Haka yake ran ki ya dad'e to aiki na ke so kiyimin duk wani motsi na Fulani k'arama ki sa min ido akan"

"Angama ran ki ya dad'e".

" Shamsiyya sa talatu ta ba ta,wanna ka yan"

"To mommy".

" Allah ya k'ara arziki ran ki ya dad'e, duk abin da ki ke so haka za'ayi Fulani"

Jakadiya sai godiya ta ke kamar anyi ma ta kyautar Aljanna.

"Zeenat wannan wa ce irin kwalliya ce, sai ka ce aljana".

"Kai umma ita fa ake ya yi sunan ta bride's makeup fa"

"Ayyah kin ji ai,sunan kwalliyar ma na arna ne"

Dariya Zeenat ta shiga yi sannan ta ce "ba sunan arna ba ne sunan ta kwalliyar amarya fa"

Hmmm to ki ce Zeenat d'in aure takeso?"

Cuno ba ki ta yi cikin yanayin ta na shagwaba" Allah ni na aure na ke so ba, sai na zama likita na zama malama kuma"

"To yan zu dai aje a wanke fuskar nan ki zo ki je ki wai wa Baban ki abinci, sai ki shiga cikin Gidan ki gaishe su.

" Allah umma ba nason shi ga cikin Gida, ni tsoron su nake ji,ba re ma Fulani ta tsakiya"

"Ki dinga addu'a idan za ki shi ga kin ji, kuma ki kama kan ki banason rawar kai"

"To umma".

Buta ta d'auka ta wanke Kwalliyar tas, sanan ta d'au kwanon ta fita.

Rona,da Lamma cikin firgici su ke kallon saurayin da ya buge Lantan.

" waye kai da za ka fad'o ma na Gida?"

Bisi ya yi murmushi ya ce "ina jikin gidan nan na ji kuna magana duk abin da ke faruwa ina ji, me yasa ki ka b'oye y'ar ki a gida?

Rona da ta fara kuka ta shiga zayyane ma sa dalilin su na b'oye y'ay'an ta har biyu cikin gida.

Ajiyar zuciya Bisi ya yi" kinyi gaskiya nima ba zan tab'a to na muku asiri ba"

Kallon Lantan ya yi da kan ta ya fashe yace" Ku kawo ruwa, suma ne ta yi yan zu za ta tashi"

Da gudu Rona ta d'ebo a koko ta kawo Bisi ya watsawa Lantan.

A firgice ta farka, amma kuma kamar ba a hayya cin ta take ba.

Rona ta kira sunan ta ko za ta amsa"Lantan"

"Lantan" Lantan ta maimaita duk abin da aka ce to shi ta ke maimaitawa.

Rona ta ji dad'in wannan matsalar da ta sa mu Lantan dan ta san muddun Lantan ta fi ta, to kuwa sai Gidan sarki Gannami kai rahoto.

"Yaro mungode da ka temake mu K'ainani ya temake ka"

Bisi kallon Lamma ya yi yace "kin ce su biyu ne ina d'ayar?

Rona ta kama hannun sa zuwa cikin d'akin da Hantsi ta ke.

Kamar kullum ta na kwance ba abin da ya dame ta,duk abin da ake ta na jin su amma ko a jikin ta.

Ganin su tare da ingarman Namiji ya sa ta ji tsoro,dan tun da take a rayuwar ta ban da mahaifin su Lu'u ba ta tab'a ganin irin halittar ba.

Bisi mamakin kyaun ta ya ke tun da ya ke a garin Duhuwa bai tab'a ganin kyakywa irin Hantsi ba,dan ko Lumma ba ta kai Hantsi kyau ba.

" kagan ta sunan ta Hantsi ita ce k'arama"

Bisi da baya jin abin da Rona ta ke fad'a ya sa ya ce"ki ci gaba da b'oye ta, ni ma zan ta ya ki dan in har Hazid ya san da su to kuwa zai k'wace su ne ko ta wa na hali"

Motsin shigowa d'akin su ka ji,duk kan su su ka juya ganin L.....

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

Story &Writing

By

R.Hussain and Noory.

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

Wannan *Littafin* *na kud'i ne* *Normal group* *N300*

VIP N500

Ki biya ki *karanta cikin* *aminci*

For more information

08107916039

.....Yau ne jajiberan bikin shekara a masarautar Duhuwa,kowa ya na ta hidima da had'a Sabon kwalki mata ma su na ta k'ok'arin samawa iyalansu kyakkyawan abinci da abun sha, dangin su ayaba da gwanda da tuwon acca dan shekara - shekara ake had'a wannan abincin.

Sarki Gannami ne zau ne a fadar sa, mutane sun yi sahu - sahu kamar koda yaushe. Tsaye ya ta shi ya kalle su dama da hagu"hahhhhahhhh hahhhhh"dariya ya sheka sannan ya murtike fuska kamar ba shi ya yi ba."K'ainani"

Gaba d'ayan fadar su ka amsa"K'ainani" su na masu nutsuwa da mik'a wuya da bud'e hannuwa kamar yadda su ke ko da yaushe.

Hazid kuwa kallon matan fadar ya ke d'aya bayan d'aya ko zai dace da budurwar madubin tsafin sa.

Cikin dandazon matan kuwa Lamma ce daga can sawon masu aure,kugun ta sanye da jan walki na Rona,jikin ta kamar aljana ta yi bak'ik'irin fuskar ta ta yamushe da ruwan dafaffan rogon da k'aro da Rona ta mulke ta da shi, ta yi mu ni sosai. Dan a matan ma ba wacce ta tsaya kusa da ita,natural skin d'in ta b'ace,ba'a ganin komai na ta sai pink lip d'in ta da fararen idonta.

Sarki Gannami kawai ta ke kallo mamakin girmansa da munin sa ta ke ga uban dogon hauren giwa jikin k'wallen kansa, ya zama kamar dodon aljani.

Hazid gaba d'aya rasa nutsuwar sa ya yi,ganin budurwar madubin tsafin sa ya ke kamar a cikin matan da su ke fada zai iya ganin ta, kullum idan a ka zauna fada sa rai yake, k'anshin jikin ta ya ke ji a zahiri,muzurai kawai ya ke yi. Ganin ba shi da mafita rik'e kan sa kawai ya yi, k'ara ya k'walla ya na jujuya kan sa.

Ganin haka yasa matan fada fara neman tsira,Lamma da ba ta tab'a ganin hauka ba, ba ta san da ta gigice ba ita ma k'ara ta kwalla.

Cikin gigita Hazid ya diro,jin muryar da bai tab'a ji ba kusa da shi,wajen matan ya nufu ya yin da kowacce ta ke neman hanyar guduwa,dan idan Hazid ya kama ki a haukan sa sai ya kashe mutum.

Sark'a aka je fa masa aka fara nad'eshi da ita,ihu ya ke ya na son ya k'wace, harshen sa ya ke taunawa jini ya na ta sharara.

Sarki Gannami da Shiwu sun fi kowa shiga tashin hankali, ganin wannan ciwon na Hazid ya k'i warke wa,kullum k'aruwa haukan ya ke.

Boka 'Dundumi ya ce "zai warke kamar be tab'a hauka ba.Amma me maganin ba'asan san da zai bayya na ba,kuma zai zo da sabbin al-amura wan da 'yan Masarautar Duhuwa ba za su tab'a amince wa ba,kuma shi ma ashirye ya ke da ya dakatar da zuwa su garin na su.

Lamma tun da ta sami hanya gudu ta ke, Rona na bin bayan ta dan kar ta b'ace kuma asiri ya Tonu,wata hanya ta bi hankalin Rona ne ya tashi ganin wasu matasa su biyu a jikin gidan su.....

SUDEES

" Ummi Prince ya fad'i a filin Polo daga kan doki ya fad'i yan zu ba'a san a wana hali ya ke ba " gaba d'aya a gigice ya ke.

"Kwantar da hankalinka yaro, prince Zaid zai samu sauk'i inshaallah kai dai ka ci gaba da yi ma sa addu'a".

"Lahaula,walak'uwata illah billah,Allahuma lah sahla illah ma ja'altahu salha wa anta taj'alul haznu izah shi'ita sahla"

Haka ya ke ta maimaitawa har ya sami mutsuwa.

Wayar ya k'ara dakkowa,kiran Hibbullah ya yi,cikin sa'a ta shiga "Alhamdulillah ta shiga"

A can England kuwa Hibbullah du a rud'e ya ke ganin wasu injina da a ka sa Prince a ciki kuma be farfad'o ba, couch d'in su ma sai strongly ya ke a hospital d'in tuni police sun cika hospital d'in dan kulawa da tsaron Prince Zaid.

Ringing ya ji wayar sa na yi ganin Sheik Sudees ne ya sa ya yi picked call d'in"ya sheikh "

"Hibbu ya Prince d'in?"

Cikin aro dakiya ya ce"Alhamdulillah da sauk'i,doctors d'in ba su fito ba har yanzu"

"Innalillahi wa'inna'ilaihirrajiun, duk abin da ake ciki ka kira ni pls"

"Inshaallah sheikh"

Ajiye wayar ya yi.

Ya kalli Ummin nasa"kin ji abin da Hibbullah yace?"

"Ka kwantar da hankalin ka,zai sa mi lafiya"

Mark kuwa tun da police su ka ta fi da shi, ba wanda ya bi ta kansa, kulle shi akayi cikin d'aki me duhu da zafi dan kowa yasan waye Prince Zaid.

"Allah ka sa Zaid ba zai ta shi ba,Allah ka sauk'ak'amin aiki na, ya fara mutuwa ba tare da na wahala ba"

"Hahhhhh amin aunty kin ga kuwa Inda na yi a fada?"

"Hahh ai nasan ka Lukman makiri ne kai"

"Ai ingayamiki, har sarkin sai da ya tausayamin kamar fa zan yi hauka hahhh"

"Kasan Allah da zanga wanda ya yi masa haka ko,sai na yi masa kyauta me nauyi"

Fulani babba kuwa zaune ta ke ta mik'awa Allah Lamari ta, fatan samun sauk'i ta ke wa d'an nata, Jakadiya na zaune a k'asa ta na ta matsar idanu, ta na karantar halin da Fulani ke ciki. Ganin ba ta gane komai ya sa ta fita guntsa wa Hajiya Samira gulma.

Juya wan da za ta yi taga an shigo da Safwan ranga -ranga kamar gawa.

Saurin komawa ta yi ta ji me ke faruwa kuma.

"Allah ba ka lafiya d'an sarki jikan sarki"

Jin kirarin nan ya sa Fulani d'ago kanta ganin Safwan a jigace ya sa gaban ta fad'uwa "ya Allah

Zan rasa 'ya'ya biyu a lokaci d'aya Allah ka kawo min sauk'i"

Ido Jakadiya ta k'ura mata,dan ganin ya fulanin za ta yi.....

Littafin kud'i ne ki biya ki karanta *cikin aminci* .

Allah baya yafe *hakkin wani akan wani.*

Za'a k'ara yawan typing da zarar mungama free pages.

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

Story &Writing

By

R.Hussain and Noory.

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

Wannan *Littafin* *na kud'i ne* *Normal group* *N300*

VIP N500

Ki biya ki *karanta cikin* *aminci*

For more information

08107916039

Page 9

....."Aunty na tsani ingan ki cikin damuwa,nasan matsalarki dai akan Fulani babba ne da 'ya'yan ta,to Wallahi kaf gidan nan natsani naga wani acikin sa da sunan masarauta a tare da shi, ciki kuwa har da wannan d'an ji ji da kan Zaid,Aunty na shiga jikin sa ne dan na san ta yadda aikin mu zai ta fi, ba tare da mun sami wata matsala ba"

"Yauwa yaro na ina alfahari da kai,Yan zu nasan ka had'a jini da masarautar mu ta Sudan"

"Hahhh hahhhh Aunty dole ne burin ki ya cika amma ki san yadda za ki yi ki haihu acikin gidan nan. Idan ba haka ba kuwa, mu na ji muna gani mulki zai gagare mu a k'asar nan"

Fulani ta uku wato Samira tunanin mafita ta shiga yi.

"Tabbas dole ne in yi ciki,Kuma in haifi magajin sarki".

Wayar Lukman ce ta ke Ringing ganin Prince Zaid ne ya sa ya yi tsaki" mtsww"

Picked ya yi "Assalamu Alaikum ran ka ya dad'e, yan zu na ke zan cen ka a zuciya ta"

Daga can kuwa murmushi Prince Zaid ya yi masa ya na jin k'aunar Lukman d'in har cikin ran sa.

"My bros yakake, nima ji na yi ina kewar ka shiyasa na kira ka"

"Wayyo 'Dan uwa Wallahi Prince lafiya lau na ke, ga Aunty Ku gaisa.

Da ido ya nuna wa Samira ta saki jikin ta su yi magana.

" Hello my Son"

"Mami I miss you,yakike ya gidan?"

"Lafiya lau mu ke Prince ya England, yau she ne dawo war ne?

" To Mami gamu nan dai,mu na ta shirye - shirye dai, but very soon we will back inshaallah "

"To Allah ya kawo Ku lafiya my Son"

"Amin amin Mami"

Ga 'Dan uwan na ka,mik'awa Lukman wayar ta yi.

Ta na hararar wayar da mugun tsana, "bros ya wasan hope normal dai ko?"

"Normal Wallahi Lukman"

"Mashaallah, bros bye" yan ke wayar Prince ya yi"Oh my God, gaskiya ina kewar ku my family".

Fuskan tar wasan da ke gaban sa ya yi,wayar da ya yi da Lukman ce ta k'arfafa masa gwiwa.

San ye ya ke cikin shigar su ta Polo ya sa white clothes stick d'in sa ma white ya kama dokin sa Don ya d'ane, ya yi matuk'ar kyau sai hoton sa ake d'auka.

Wannan abu shi ne ya k'ara hassala zuciyar Mark, captain d'in su ne ya daga flag sanan ya ajiye, a sukwane da wakan su ka fara gudun tsere,Mark ba burin sa team d'in su ya ci ba, burin sa ya kada Prince Zaid daga kan dokin sa,ya bi ta kan sa ya take shi.

Prince da ya tsere abokan takarar ta shi ya kusa zuwa ending line kenan,Mark ya jefawa dokin Prince sandar hannun sa,ta ke dokin ya hantsila da Prince Zaid, fad'uwa ya yi a sume.

Mutane su ka fara challenge akan wannan wasan,Police ne su ka yi arrest d'in Mark su ka tafi da shi.

Ma'aikatan lafiyan da ke gurin ne su ka d'auki Prince su ka sa shi a ambulance su ka fita cikin sauri.

Hibbullah da ya bi su cikin sauri ya na tunanin me Kuma Prince ya yi wa Mark, har da ya ke farautar rayuwar sa.

Hankalin sarki Abdurrahman ne ya tashi, tun da ya ga wasan live a ka nuna shi.

"Kira Hibbullah mu ji,Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un"

Fulani babba kuwa kuka ta ke ta na cewa"ni dai aje a tawomin da shi, banason wannan wasan kasadar da Zaid ya ke yi amma ya k'i ji"

Samira da Hafsat kuwa murna su ke kamar sallah.

Lukman ne ya shigo a rikice"shikenan sun kashe shi wayyo 'Dan uwa na"

Ihu ya ke a fadar me martaba kamar gaske. Kama shi fada wa su kayi aka shigar da shi ciki.

Safwan ma ya na can wani big park shi da wata budurwa bai san abin da ake ba, sai da shukurah ta kira shi, kuka ya ke yi yana kiran Hibbullah wayar ta k'i shiga saboda kowa neman layin ya ke.

A ko ina sai k'ara haska fad'uwar da prince ya yi a ke yi BBC da sauran social media,ganin ake ma kamar ya sami matsala.....

Sudees ma hankalin sa a tashe ya shiga kiran Hibbullah,jin ba ya tafiya ya Safwan ta na Ringing amma ba'a dauka.

Kawai addu'a ya shiga yi wa Prince, Hamza ma sai fatan sauk'i ya ke nema wa Prince.

Serah kuwa sai hauka ta ke,ta na sai ta kashe Mark,tun da ya tab'a ma ta Prince,Baban sa Johnson shi ne ya ke tausar ta, Hospital d'in da aka kai Prince ya kai 'yar ta shi tilo.

Bilkisu kuwa kuka ta ke yi ta na rok'on Mahaifiyar ta su Hajiya Amina a yi mata Visa ta je wajen su.

Ikon Allah ne kad'ai ya kawo Safwan cikin Masarautar har amai ya ke yi tsabar kuka ya na parking kuwa ya fi to kenan ya fad'i sumamme.....

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

□□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

Story &Writing

By

R.Hussain and Noory.

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

Wannan *Littafin* *na kud'i ne* *Normal group* *N300*

VIP N500

Ki biya ki *karanta cikin* *aminci*

For more information

08107916039

□ page 8

.....Boka 'Dundumi ke ta wasu surutai na tsafin sa, wata k'atuwar ungulu ce ta bayyana a gaban sa,ta bud'e fuka - fukin ta,hannun sa ya bud'e ta hau kai.

"Ki je ki zaga duniya ki gano min su waye za su shigo Masarautar Duhuwa " ta shi Ungulun ta yi ta Lula sararin samaniya.

Ci gaba da bincike ya yi,cikin halwar tsafin sa,tabbas wannan abu sai ya faru, k'ara kallon kwaryar ya ke ya na kallon mutane ma su cikakkun sutura a jikin su kan su sanye da rawani,wan da ya b'oye ainahin fuskar su.

"Ahhhhhhhh na rantse da k'arfin tsafi na sai na dakatar da ku,nu na kwaryar ya yi da sandar sa ta tsafi ta ke mutanen su ka b'ace.

Zarya ya shiga yi,'Dundumi a duk'e ya ke tsabar tsufa,amma jin sa ya ke kamar d'an shekara asirin da biyar burin sa ya gagari kowa a duniya.

Ungulu sai wa ni haske ta ke bi, sai ta kusa cin ma sa sai ya b'ace ma ta,haka tai ta zagaye a sa ma k'arshe dawo wa tayi ga 'Dundumi ganin ta haka ya sa ya bud'e hannun sa ta hau,kallon ta ya ke kawai ya damk'e hannun sa ta ke ta b'ace.

Lantan ce ta shiga d'akin Bisi ne ya ce " Rona kai ta gida"

Lantan ma ta maimaita.

"To Bisi zo mu fita tun da ka gan su ni dai ka temaka ka rik'emin sirri na"

"Ni ma sun zama sirri na zan kula da su fi ye da yadda zan kula da rayuwa ta K'ainina ya temake mu"

Yau saura kwana Biyar bikin shekara a garin Duhuwa,Masarautar ta cika da matsafa kala -kala dan bikin cikar shekara, a wannan kwanakin ake neman mazajen da za'a ba da hadaya ga dodon tsafi k'ainani.

Bilkisu ce ta ke waya da babban yayan ta Hibbullah so ta ke ya ba wa Prince Zaid su gaisa amma Hibbullah ya k'i.

Saboda ya gama ga ne k'anwar ta sa ta fad'a a tarkon k'aunar Prince d'in, sanin waye Prince Zaid ya sa bayaso k'anwar sa ta fad'a mawuyacin hali,dan gani ya ke Prince ba zai tab'ason mace ba,saboda wulak'ancin da su ke fuskan ta awajen sa.

"Yaya Hibbu ka ba wa prince mu gaisa"

Had'e fuska ya yi kamar ta na ganin sa "baya Ku sa da ni "

"Okay ni in na kira ba d'auka ya ke ba ta k'arasa magana cikin sangar ta irin ta 'ya'yan masu mulki.

Kashe wayar ya yi dan ba zai so alak'ar su ta rushe ba.

Stadium d'in cike ta ke da fans d'in teams biyun 'yan Oxford da Ku ma y'an UK ne za su yi wasan Polon, Prince ya na d'aya data cikin wad'an da za su yi wasan. Dokin sa me suna Don ya ke shafawa.dokin irin na k'asar Brazil ne.

Haka kawai Prince Zaid ya ke jin kamar wani abu zai same shi a filin wasan, dan gaba d'aya ba ya jin karsashi a wajen.

Hibbullah ne ya k'ara so kusa da Prince d'in.

"Prince ya dai?"

"Nothing"

"Are u sure?

" yeah"

Tun da 'yan Uk su ka shigo,wani acikin su me suna Mark ya tama wa Prince ya ci burin sai ya hallaka shi kowa ya huta, ya za'ayi ya zo k'asar su kuma ya fi su d'aukaka.

Saura five minutes a fara wasan sa da zumuncin tsakanin students d'in.

Don an had'a wasan ne dan nishad'i da karfafa zumunci tsakanin makarantun biyu.

Timi ne ya ma ke wata yarinya dan ya aikata ma ta abun da zai kub'utar da abokin sa Bisi.

Bisi na saman bishiya ya na kallon abin da Timi ya ke yi, rufe idanun sa ya yi lokacin da Timi ya dage walkin sa da na budurwar ihu ta ke sosai,Bisi jikin sa har rawa ya ke dan tausayi, shi dai baya son wannan al'ada ta garin Duhuwa.

Sai da Timi ya gama ya kira Bisi ya sakko daga kan bishiyar, nu na masa ya yi da ya d'age walkin sa,mutane su zo su gan su.

Girgiza ma sa kai ya yi alamar ba zai yi ba. Haka Timi ya hak'ura ya je ya na nuna wa mutane Bisi da yarinyar sai dariya ake yi ana ta ya Bisi murnar kub'uta daga hadaya dan har an fara nuna shi a gari.

Hawaye ne ya taru a cikin idanun sa, tausayin yarinyar da Timi ya yi wa fansar hadayar sa ya ke ji, Kuma ba ta ga fuskar ko waye ba dan ta baya ya buge ta.

Iyayen Bisi ma sai rawa su ke tik'a d'an su ya tsarkaka haka a ka d'auki yarinyar a ka, ana ta yawo da ita dan ba k'aramin dace ta yi ba da Bisi ya zab'e ta ya fanshi Kansa da ita.

Shi yagaji da wannan murnar da ake ta yi masa,sulale wa ya yi ya nufi gidan su Hantsi.....

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

Rubutawa da Tsarawa

Na

R.Hussain da Noory

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

Littafin kud'ine,

Normal group N300

VIP N500

domin k'arin bayani ki tuntub'emu akan wannan Number 08107916039

Free page12

.....Ummi ce ta ke jin labarai a k'aramar radio wadda ta ke kan mudubi, ba ta rabo da jin labarai.

Harun ne ya shigo d'akin na ta"Assalamu alaikum" jin sallar d'anta na biyu"wa'alekumussalam".

"Ummi bar ka da warhaka" amsawa ta yi "bar ka dai Harun". Dama so nake ki gayawa Abba inason koma wa makaranta wani satin".

Ummi ce ta ce cikin mamakin hutun da kamar yau ya dawo wai har an koma" yanzu Harun har an koma? Ikon Allah, Allah ka sa mudace, ya na babban falo a waje ka je ka same shi mana".

Harun ne yace "to ummi nagode" duk sanda zai koma makaranta sai ya ji kewa ta kamashi, amma ya godewa Allah tun da ya kusa kammala karatun na sa na likitanci.

Da Sudees ya had'u "ya sheik" Harun ya fad'a cikin tsokana.

Sudees ne cikin murmushi yace"kai ma ko Harun,kar ka manta dai sunan Abba ne" dariya Harun ya yi ya mayar masa cikin barkwanci dan yanason Sudees ya dinga sakewa da shi,"magajin malam,ai malam ne" murmushi kawai Sudees ya yi, ya wuce wajen ummin ta su.

A can falon k'asa kuwa Amal ce da yusra su na yin assignment d'in da aka ba su a makaranta ko wacce ta bage text book d'in ta na Biology ta na ta zanen animal cell dan shi aka ce suyi tare da labelled d'in sa.

Ko wacce so ta ke, ta samu maki sosai ko magana ba sayi sun nutsu su na ta yin aikinsu.

"Assalamu Alaikum"

Wata kyakkyawar budurwa ce ta shigo falon na su, doguwa ce sosai,siririya, abaya ja ce a jikin ta,ta yi rolling da mayafin ta yi kyau sosai.a tare su ka d'ago dan amsa ma ta

"wa'alekumussalam,lah Aunty Sultana oyoyo duk kan su, ta shi su ka yi suka rungumeta.

Cikin jin dad'in k'annen Sudees su na k'aunar ta, ta ce mu su" ina umma na gan ku Ku kad'ai?"

Amal ce ta ce"ta na ciki, aunty Sultana sannu da zuwa"Yusra ce ta nu na mata gurin zama dan duk a tsaye suke. "Bari in kira miki ummi" Yusra ta tafi kiran ummin na su.

Kallon Amal Sultana ta yi tace"Yananan kuwa my sister ?"

Amal ta waske irin ba ta san wa take magana akai ba ta ce "waye fa?"

Hararar ta Sultana ta yi tace "kin rainani Amal da yawa to ya sheik Sudees" murmushi Amal ta yi tace yan zu ya shiga wajen Ummi".

Dad'ine ya kama Sultana burin ta ta ganshi ko ta sami sauk'in darad'ad'in son sa da zuciyar ta take mata.

Ganin ya na tawo wa falon cikin jallabiyar sa milk colour kan sa ya sha gyara sai k'walli ya ke, sajen sa da ya kewaye fuskar sa shima sai k'walli ya ke ido Sultana ta zuba masa kamar za ta cinye shi.

Abin da ya tsana kenan a rayuwar sa kallo, musamman ma mace ta k'ure sa ido. Tsaki ya yi a cikkin zuciyar sa dan jikin sa ya ba shi kallon k'urullah ta ke masa. Zancen zuci ya ke na rashin kunyar 'yanmatan zamani. Da suke iya nuna maitar su a fili akan namiji, ji ya yi ance " ya Sheik ina wuni" cikin muryar iyayi da kwarwasa.

Dakewa ya yi ya amsa"lafiya" bai jira ta k'ara magana ba ya wuce taron da zasuyi da y'an k'ungiyar JIHAD DA'AWA FOUNDATION wan da wasu za su je k'asar Morocco dan kira ga addinin Muslunci,wanda Hamza ne shugaba a tafiyar bayan sati d'aya kuma Sudees zai bisu. Inshaallah

Cikin hawayen so da jin matsananciyar k'aunar Sudees a zuciyar ta Sultana ta ce"Amal ina k'aunar 'Dan uwanki sosai rasashi a rayuwa ta dai dai ya ke da r.... Maganar ce ta katse jin muryar Ummin su " mashaallah yau Sultana ce ta ziyarce mu"

Saurin share hawayen ta,ta yi murmushi yak'e ta shiga yi wa Ummi "eh Wallahi" Sultana ta fad'a Yusra da ta san me Sultana ta ke wa zuwa ta ce"hummm Ummi ai....,.....

DUHUWA

k'ara Hantsi ta kwallah ganin Lamma a haka dan ita ba ta san 'yar uwar ta ba ce ta shigo d'akin da wannan kamar,jikin ta ya yi bak'ik'iran da shuni da k'aro da ruwan rogo,ta yayya mushe,dole ta ji tsoron ta a haka.

Bisi ne ya shigo d'akin da sauri ganin Hantsi a rakube jikin ginin icen kaban ta had'a kai da gwiwa jikin ta sai rawa ya ke. Lamma ce ta ce"Hantsi ni ce fa" Bisi ne ya katse ta da cewa "ki mana shiru ai dole ta ji tsoron ki lamma waye zai san ke ce a haka?".

Rona ce ta k'araso d'akin ta na tambayar "lafiya" ganin Lamma a d'akin ya sa hankalinta ya kwanta.

Bisi ne ya fito dan yau 'yanmatan gidan a burkice su.

Lamma ce ta ce "Rona da ma haka MASARAUTAR MU take? Na rantsi da k'ainani ba zan k'ara

  zuwa ba".

Murmushi Hantsi ta yi tace" me ki ka gani a can d'in Lamma"

Lamma da jikin ta ya fara damunta da k'aik'ayi sai soshe soshe ta ke k'wallen da aka kare ma ta k'irjin ta cire dan ya dame ta da k'aik'ayi duk shuni da k'aron sun manne mata a jiki.

Rona ce ta ce"Lamma da ma banso ki ka ce za ki je ba,banaso ki nemi abu a wajena na kasa yi miki ne,shiyasa na kai ki fada yau"

Hantsi ce tace" amma Lamma kin tsoratani"

Lamma tace"to yi hak'uri Hantsi".

Ganin ta cire komai na jikin ta sai soshe - soshe ta ke ya sa Rona kama ta su ka shiga wani kewaye dan ta wanke mata jikin ta.

Lu'u ne ya shigo gidan ransa a b'ace tun a fada ya gane Lamma duk da shigar da tayi "Rona kin kyauta"

Lamma ce ta wuce d'akin su dan bataso ta ji fad'an da za'ayiwa Rona akan ta, walkin ta ta daura ta rufe k'irjin ta da k'wallen ta na 'yan mata.kwanciya ta yi dan har yan zu a tsora ce ta ke da ganin sarki Gannami da d'an sa Hazid.

Boka 'Dundumi kuwa rawa ya ke ta yi ya na surutan sa na tsafi hajijiya ya ke sannan ya zauna a k'asa dab'ar, wata kurciya ce ta sakko ta tsaya a kan sa.

Ciro ta ya yi ya rik'e ta a hannun sa "hahh hahhhh hahhhhh ba'abin da zai gagari shugaban matsafan duniya dole in dakatar da matasan nan da yunk'urin su na shigowa MASARAUTAR MU, ki je ki samo min labarin samari shida wad'an da suke k'ok'arin hana cikar burina ki ga no min wanne magani za su zo da shi,sai na lalata tasirin sa" b'at kurciya ta b'ace.

Wannan littafin *na kud'ine ki biya ki karanta cikin aminci*

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□MASARAUTAR MU□□□□□□

Story & writing

By

R.Hussain and Noory.

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

Wannan littafin *na kud'i ne ki* *biya ki karanta* *cikin aminci*

Normal group N300

VIP N500

For more information 08107916039

Free Page 11

.....Tun da aka shiga da prince Zaid emergency Ward likitoci su ke ta aiki akan sa.

Kusan minti talatin da takwas da sarewar su akan zai farfad'o nan kusa, duk sun karaya sun d'auka ya shiga doguwar suma wadda zata d'au watanni bai dawo ba.

Dr.Danial ne ya ga farfad'o war sa, da sauri ya nuna wa sauran likitocin.

Danial ne yace "hi prince"

Ganin su ya yi duk sun had'a gumi ga firgici a idanunsu.

Murmushi ya sakar musu dan su kwantar da hankalin su,tambayar su ya yi ina Hibbullah?"

K'ok'arin zare drip d'in hannun sa ya ke dan ya san abun azahiri a ka nu na ko ina anga abin da yafu.

So ya ke ya yi magana da mai

 martaba da mahaifiyarsa yasan sun gani,dan duk wani wasan Polo da zai yi su na gani.

Dr. Roshan ne ya dakatar da shi"yi hak'uri yarima ka na buk'atar hutu.

Prince ne yace"ka kira min d'an uwana,inason ganinsa ne".

Doctor Denial ne ya fita da kan sa,tare da Hibbullah su ka shigo.

Da sauri Hibbullah ya je kusa da prince Zaid ya na tambayar sa ya jikin nasa"Prince ba wata matsala, bayan ka ma lafiya ya ke?".

"Kai dallah ka dame ni, baka gani ba ne eye?"

Dariya Hibbullah ya yi cikin farin ciki da jindad'i "Alhamdulillah" waya ya d'akko mai martaba ya kira.

Ringing d'aya yaji an d'auka.

Mai martaba ne ya d'auka yace "Assalamu Alaikum Hibbullah ya Zaid d'in?"

Zaid ya mik'awa wayar "ina lafiya mai martaba".

" Zaid ba abin da ya same ka dai ko?"

"Alhamdulillah ba komai Allah ya taimakeka".

Hira suka d'an tab'a da mahaifin nasa,sannan su ka yi sallama.

" me ka yi wa wancen arnen ne ya ke harin rayuwar ka Prince? "

"Mu tafi gida lawyer sai ka ji me na yi,Tun da naga aikin da ni yau za'a fa ra ko"

"Matsalarka kenan Wallahi, ba dama ayi serious talking(magana ta gaskiya) da kai sai ka kawo wasa a ciki,ai shikenan".

Likitocin da tun d'azu sun bar musu d'akin, saboda ganin prince da Hibbullah ne su ke magana (kunsan turawa ba ruwan su da gulma).

Likitocin sun so ya zau na ayi masa gwajin k'wak'walwa Prince ya ce bayaso,haka su ka hak'ura aka kai shi gida.

A can masarauta kuwa, kowa ya ji wannan labarin wasu na farin ciki wasu na bak'in cikin faruwar wannan lamari.

Zeenat ce zauna ta na ta kuka cew ta ke" yan zu shikenan bazan gan shi ba, an kashe shi umma?"

Umma ce tace"ke banason sakarci haka aka ce miki an kashe shi ne?"

"To amma umma doki ne fa ya nanashi da k'asa kin ga girman doki kuwa?"

"A'a ban gani ba,ke ki ka gani, ki rufe min baki yariman ma da bai san ki ba".

Tashi ta yi ta shige d'akin ta, ta ci gaba da kuka " Wallahi da nasan wan da ya ka da prince Zaid da sai na rama masa"

Addu'a ta ke ta masa kala - kala na neman masifa.

Sarkin dawakai ne ya shigo gidan cikin alhinin wannan lamari,"Assalamu Aliakum"

Umma ce ta amsa " wa'ale kimussalam sannu da zuwa malam"

"Yauwa Rumasa'u ya gidan?"

"Lafiya lau"

"Ina Zeenatu ta ke ne?"

"Hmmm aiki ne ya sa me ta ai,ta na ciki tana kuka"

"Subhanallah kuka kuma,me ya faru?".

"Doki ya ka da yarima,shi ne ta zauna ta na cewa an kashe shi, fad'a ne kawai ba za'a yi ba" murmushi malam Ibrahim sarkin dawakai ya yi.

"Zeenatu sarkin shirme,to ai ba mutuwar ya yi ba kuma ma ance ya warke"

Zeenat ta na jin duk abin da su ke cewa.

Kamar an jefota ta fito daga d'akin"Allah baba?"

Mamakine ya kama iyayenta ganin wannan zumud'i na Zeenat.

Ganin kamar ta yi ba dai dai ba yasa tace"ni fa kawai inaso ne nagan shi ya dawo garin nan munje kai gaisuwa gaban sa"

Ta k'arasa maganar ta na turo baki.

Tun da aka shigo da Prince Safwan Fulani ta ke ta ambatun sunan Allah bayin da su ke kewaye da ita ne su ke ta fatan samun sauk'i ga Prince Safwan,su na ba su guri.

"Wayyo mun shiga uku!!! Ran ki ya dad'e dubi yarima k'arami mun ga rayuwa yau"

Ta na yi ta na kula da yanayin Fulani.

"Wata baiwa ce kusa da ita a durk'ushe ta na jiran umarnin Fulani.

"Je ki d'akko ruwa"

Cikin danne damuwar ta,ta ke bada umarni.

Kafin ta gama fad'a ankawo ruwan roba, da kan ta,ta tashi hannu ta mik'a aka zuba ma ta.

Fuskar Safwan ta shafa da ruwan ta d'ora kan sa a cinyar ta,waya sallama ya kawo mata Prince Zaid ne a kan layi.

"Allah k'ara lafiya ran ki yadad'e,babbar giwa kin fi k'arfin

k'anana - k'anana

Yarima ke magana"

Jin haka ya yi dai dai da far kawar Prince Safwan.

Jikin ta na rawa ta sa aka d'aga mata wayar"Zaid"

Ajiyar zuciya ta sauke,jin sallamar d'an na ta, Safwan ne ya yi sauri ta shi "Prince kana lafiya?"

Daga can b'arin Prince da ke kwance a Royal bed d'in sa ya amsa "Ina lafiya Safwan ya Ku ke?.

"Alhamdulillah Zaid,ya jikin naka?"

Fulani ce ta ke magana kasan cewar ba kowa a falon na su duk bayin sun fita dan ba ta guri ta gana da prince d'in.

"K'alau nake mommy na"

"To Alhamdulillah ka dai dinga kulawa Zaid"

"Inshaallah mommy" haka su kai ta hira kowa hankalin sa ya kwanta.

Lukman jin labarin Prince ya farfard'o sai da ya ji ciwon kai me tsanani ya kamashi. Samira sai kai kawo ta ke a bed room d'in ta, ji ta ke kamar ta mutu da jin wannan bak'in labarin na Prince ya na nan da rai"Wallahi dole ne ka mutu Zaidu gani nan zuwa ga re ku"

Dun k'ule hannun ta tayi, ta na ta naushin hannun ta na hagu,sai iska ta ke fitar wa ta baki.

Hafsat kuwa da jin labari sai da ta bawa Jakadiya kyautar turmi uku, dan ita ta kawo mata labarin fad'uwar Prince Zaid. Ji ta yi kaso arba'in bi sa dari 40% na damuwar ta ya kau,dan ta gama sa ran doki ya murje Prince Zaid.

Yan zu kuma,murna ta koma ciki"indai ina raye to sai na ga bayanki Fulani Zahra'u".

MASARAUTAR DUHUWA.

Timi da Bisi ne tsaye k'ofar gidan su Lamma, dan yau duk samarin da su ka fanshi kan su,sun ta fi kamo hadayar wannan shekarar.

Bisi ne ya ce shi ba'in da zai je, shi ne ya ke son shiga gidan su Hantsi dan yasan ba sa fita ko ina.

"Bisi wai me za kayi anan ne,tun da zu ka tsayar da mu anan,ba mu je d'akko hadaya ba, kuma ba mu huta ba".

Da gudu Lamma ta ban game su ta shige cikin firgici.

Bisi da be gane ta ba ya bita cikin gidan, ganin ko wata ce zata cutar da su Hantsi.

Rona ce ta k'araso ita ma ta na haki dan gudu ba na wasa ta yi ba,ga girma shiyasa ta wahala ganin Timi

tsaye bai shiga ba

"Way.....maganar ce ta katse jin k'arar.....

Ki biya ki *karanta cikin* *aminci* .

Allah baya yafe *hakkin wani aka* *wani*

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

Rubutawa da Tsarawa

R.Hussain da Noory

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nisha dantarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

SADAUKARWA GA MASOYANMU□

Wannan littafin *kud'i ne ki biya ki karanta cikin* *aminci*

Normal groupN300

VIP N500.

2414444137

Zenith bank

Rahinat Hussain.

Za ki tura shaidar biyanki ta wannan number 08107916039

Idan Kuma recharge card ne MTN ta wannan number 08107916039 ko kuma 08145498489.

Ga matanen mu na Niger kuma, masu tura katin waya ku, tuntub'emu ta pc. akan wannan number +22796816658.

FREE PAGE 13

....."Kina jina ko Jakadiya,ba na so a sami Matsala fa" Fulani ta biyu watukun (Samira) ke k'ara jaddadawa Jakadiya.

Cikin girmamawa Jakadiya tace"inshaallahu ranki ya dad'e,ina fita zan tura k'anwata wajen malam d'in Wallahi aikin sa sha yanzu magani yanzu, Yarima da k'asar nan sai dai kallo".

Tsawa Samira ta daka wa Jakadiya,tace "cemiki na yi a hana shi zuwa ko ce mini na yi gawarsa ce zata iso nan da sati biyun da yake ikira rin dawowa?"

Jakadiya ta k'ara gurfana gaban Fulani ta biyu"tuba nake ranki yadad'e,Allah ya wuci zuciyar ki, duk abin da ki ka ce haka za'ayi".

Da hannu ta yi mata nuni da ta b'ace mata da gani.

Da Saudi Jakadiya ta fito daga b'angaren Fulani ta biyu ta na surutai"daga zuwa gayamata yarima ya samu,shikenan sai kuma ki huce a kaina? hmmm ba in da zani Wallahi Allah ne ya bani hanyar tara kadarori ".

A b'angaren sarki Abdurrahman kuwa jin komai ya dawo dai - dai ya tilastawa waziri Alhaji Usman mahaifin Hibbullah yin Visa, don ya tawo da su Prince Zaid, mai martaba gani ya ke kamar yan zun ma kawai sun fad'a ne ba dawowa za su yi ba.

Fulani ta uku wato Hafsat 'ya ga sarkin Sudan ke ta kai komo tsakanin kudu da arewa, Lukman da wutar k'iyayar Prince Zaid ke k'ara ruruwa a zuciyar sa,ya kasa ko da motsi Jakadiya da ta kawo rahoton samun sauk'in yarima Zaid na rakub'e a gefe ta na k'ifta idanun munafurci.

Lukman ne ya yi k'arfin halin cewa" yan zu Jakadiya Fulani ba abin da tace,game da lamarin?"

K'ara durkusar da kai ta yi sanan ta ce" ai ranka ya dad'e inda kasan ba ita ta haifesuba haka ta yi,dan ranga - ranga aka shigo mata da yarima Safwan amma matannan ko fargaba ba ta ji ba".

Fulani ta uku ce ta ce"taya za ta ji fargaba,ta sami manyan bokaye sun tsaya mata,Wallahi ni Hafsat sai na sa Zahra'u hauka a gidan nan"

Wani tunanine ya zowa Lukman da sauri ya mik'e kafad'ar auntyn na sa ta data cikin rarrashi da lalami ya zaunar da ita,sannan ya ce"

Aunty in dai Kinga burinki bai cika ba,to ki k'addara ba na numfashi a duniya".

Cikin zafin nama ya mik'e "dole ne ki samo mana magajin sarki Aunty ko ta halin k'ak'ane"

Fulani ta uku ce tace"Lukman ta ya ya? Zan samu ciki har na haihu alhalin kasan ba na haihuwa".

Jakadiya da ta ke jin abi da su ke fad'a , sai da ta jinjina musu.

"Dole ne ki yi cikin k'arya har ki haihu,ni kuma zanji da samo jaririn da zai zama magaji wannan alk'awari na ne"

Jakadiya tai saurin cewa"ina tare da ku d'ari bisa d'ari yallab'ai".

Hafsat ce ta ce "tashi ki je, sai kuma ta dakatar da ita ta hanyar cewa" muddun naji wannan zancen a waje ki tabbata sunan ki gawa".

Saurin kama bakin ta tayi alamar rufewa tace "ni Hansa'u har abada ranku ya dad'e ai baki na k'anin k'afata".

" wuce kije"

Lukman ya sallama me ta. Godiya ta yi tare da cewa "nabarku lafiya" sanan ta koma b'angaren mai martaba dan anan ta ke zaune daga bak'in harabar b'angaren.

Bilkisu ce ta zo wajen su Fulani ta na kuka dan an hanata zuwa England wajen su Prince,shi ne ta zo ko Fulani za ta sa baki. Baiwar da take wa Fulani hidima ce tayi ma ta iso, zaune ta same su cikin farinciki dan sun k'ara yin video call da su Prince Zaid da Kuma Hibbullah.

Ganin su lafiya ya sa suka saki ransu.inubi Prince Safwan ya ke sha,Fulani na ki shingid'e a kan tum -tum.

"Assalamu Alaikum"

Bilkisu ta shigo da sallama. A tare su ka amsa mata kasan cewarsu masu sanin muhimmanci ta.

Ganin idon ta jajir ya sa prince Safwan tambayar lafiya?

Had'iye kukan da ya tawo mata tayi,duk k'usawa ta yi dan gaisuwa ga Fulani babba" Mommy bar ka da wannan lokaci"

Fulani ta amsa cikin kulawa"bar dai Bilkisu me ya fa ru?"

"Inaso zan he wajen su Yaya Hibbu ne shi ne na ke so ki rok'amin Abba na, ya bar ni na je"

Bilkisu ta fad'a cikin ladabi.

Murmushi Fulani ta yi,dan ta san abin da zai kai ta can d'in

"Hmmm haba maigadon zinare, suma ai sun kusa isowa,nan da sati biyu inshaallah, kin ji" Fulani ta fad'amata cikin kwantar da hankali.

Sannan ta ce" Safwan kira min Zaid yan zu".

Wayar sa mai kyau da tsada ya d'akko,kiran Prince d'in ya shiga yi sai da ta kusa yankewa sannan ya d'auka.

Zeenat da ta fito dan jin k'arin bayani ga me da yarima Zaid dan ba ta burin da ya wuce ya dawo ta gan shi ido da ido shikenan cikar burin ta. Had'uwa ta yi da malam Usman.wlh

"Malam ina wuni"

Zeenat ta gaishe shi, Usman da ya Ke ustaz ne ba ya rabuwa da aswaki a hannu.

Amsawa ya yi yana yaba tarbiyyar Zeenat,shi dai da zata ba shi dama da ya furta kalma mafi tsada a gare ta,amma ya kasa, tsakanin su girma ma juna ne.

"Ina za ki je ne haka?" Usman ya tambaya

"Gidan doki" ta amsa a tak'aice,sallama ta yi masa dan ta ga alamar ba wani labari za ta samu ba a wajen sa.

Ganin 'yan ajinsu Kausar da Alawiyya su na dawowa daga tahfiz d'in safe wanda ita ba ta samu zuwa ba saboda damuwa da prince, da sauri ta tare su da zancen.

"Alawiyya kun dawo"

Suka amsa mata da "eh meyasa ba ki zo ba?"

"Ba ku da labarin abun da ya samu yarima Zaid?" Su kace "munsani mana,ai ya samu sauk'i tun a jiyan ma" ganin princess Bilkisu ya sa suka zube don gaisuwa.

Tun da ta d'ora ido akan Zeenat ta j.....

Obi ce zaune a gaban tukunyar tsafin ta, wasu surkullen ta ta Ke ta yi,dan ganin ta karya tasirin tsafin Hazid dan bak'aramin shige ma ta hanci ya yi ba. Gashi dai ta na iya ganin shi a tukunyar amma tsafin ta baya kama shi, k'arshe ma jinya ta Ke kwanciya duk San da ta yi yunk'urin cutar da shi, Obi 'yar wani babban bamaguje ce da sarki ya kwace ta ya aura ta k'arfi.

Tun da ta ga sarki Gannami ba shi da abin so kamar Hazid ta k'udiri niyyar wulak'antar da shi, tun ya na k'arami kuma har yan zu ba ta ci galaba akan sa ba,dan ya fita k'arfin tsafi.

Kwance ya ke a kan gadon k'arfen sa, abun duniya ya yameshi, yan zu kawai budurwar mudubin tsafin sa kawai ya ke muradi.

Zumbur ya mik'e,wajen mudubin ya nufa ya rufe idon sa,hannun sa ya sa ya ke gewaye madubin ya na tsafin sa.

Tar ta bayyana cikin sabon walki k'yallen da ya rufe k'irjin ta ma kalar wankin ta ne, gashin ta ya rufe fuskar ta. Kallon ta ya ke yana jin sha'awar ta. Tun da ya gan ta ya ji idan bai sameta ba ya gama rayuwa.

"Ke wa ce ? Ki zo gare ni zan jiyar da ke dad'in da ba ki tab'a ji ba, K'ainani zai albarkace ki,zan mai da ki sarauniyar MASARAUTAR MU".

Surutai ya ke tayi, hango Obi ya yi tana tsafi a kan sa,dariya ya ke ta yi dan yasan har abada ba za ta yi tasiriba.ya bar ta ne sai ta wahala sannan ya kashe ta duk da tana matar sarki Gannami.

"Na rantse da gemun kakan sarki Gannami sai na mallake ki" ihu ya k'wala sai hau.....

Littafin kud'ine ki mallaki na ki dan jin yadda za ta kaya.

Suwaye za su nasara

Boka 'Dundumi

Ko bak'in da zasu shigo masarauta

Wace ce budurwar madubin tsafi?

Wa sudees zai aura ne ko da gaske ne aljana ce ta aure shi?

Burin Fulani Samira da Hafsat zai ciki?

Shin waye zai zama sarki??

Lukman zai yi nasara samu jariri magajin sarki?

Princess Bilkisu me ki me nufi ne?

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

TSARAWA DA

RUBUTAWA

NA

R.HUSSAIN DA NOORY

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.A.W

LITTAFIN KU'DI NE,KI BIYA KI KARANTA CIKIN AMINCI.

FREE FAGES YA KUSA K'AREWA

Domin k'arin bayani ki tuntub'emu ta wannan numbers 08107916039/08145498489.

Page 16

.....✍ Prince Zaid ne zaune a cikin jirgin da zai maidasu gida Niger, Hibbullah da ke ta zumud'in zuwa ya ga sahibarsa Iffah dan ya yi missing d'in ta sosai. So ya ke suyi hira kafin su isa amma ganin gogan na ku sarautar ce ta motsa,yasa ya koma gefe ya sa masa ido.

"Wai kallon me kake min ne sai ka ce maye" Prince ya tambayi Hibbu.

Dama kad'an Hibbu ya ke jira ya ce" kai da wana idon kasan ina kallonka ka ji mutum?"

Tsaki Prince Zaid ya yi, ya d'auke kansa.

Dariya Hibbullah ya shek"e da ita ya na cewa" yau sai da dogarai an koma gidan tsaro".

Abin da Prince Zaid ya tsana kenan wannan tsaron na masifa,ba dama ka fito daga d'akin ka sai an bika a baya duk in da zakaje.

"Ka na wani abu sai kace mahaukaci mtsww" Prince Zaid ya fad'a ya na k'ara k'ullewa.

"Daga fad'ar gaskiya sai a kira ni mahaukaci, to ai shikenan" daga haka kowa ya yi shiru su na ci gaba da addu'ar Allah ya sauke su lafiya.

Jakadiya ganin inuwar mutane ana isowa wajen da ta ke tai saurin sakin jikin ta, ta nufi hanya da sauri kamar shigowar ta kenan, ganin Fulani babba ce yasa ta kama kirari " taka warki lafiya babbar gwiwa a shigo lafiya matar sarki uwa ga sarkin gobe inshaallah " . A haka su ka k'arasa har bakin k'ofar d'akin Fulani Hafsa baiwar ta ce ta k'on k'wasa.

Lukman ne ya ba da izinin a shigo bud'e k'ofar baiwar ta yi, Fulani ta shiga d'akin ganin mai martaba a tsaye ya na shirin barin d'akin.

"Allah k'ara lafiya da Nisan kwana ya mai jikin" Fulani da ta ke gaban mijin nasu sarki Abdrrahman ta fad'a.

'Daga kai kawai ya yi sannan ya amsa"Alhamdulillah,ta samu bacci ma"

"Allah ya k'ara sauk'i" tace.

Lukman ya gaishe ta cikin girmamawa tamkar mahaifiyarsa haka ya ke bala'in yi wa Fulani biyayya.

Ya mai jiki tai masa ya amsa.sannan su ka fito gaba d'ayan su, Fulani da Lukman su na ta ke wa sarki bayansa, su na fitowa Jakadiya da sadiya baiwar Hafsa da baiwar Fulani su ka ta ke mu su baya.

Suna fita fadawan sarki su ka koma ba kin aikin su, Fulani da bayin su su ka wuce part d'in su, Lukman ya koma part d'in sa. Dama so ya ke ya keb'e ya kira Likita dan me zai ce sai gobe bayan gobe ake sa ran dawowar bak'in shegen nan da wannan d'an sa idon munafukin abokin nasa, kiran likitan ya yi dan ya ji meyasa ya yi hakan?

Likita ya na gidan sa ya na ta farin cikin arzikin da ya samu rana d'aya, ya ji kiran Lukman da rawar jiki ya amsa duk da lokacin k'arfe 12:30am na dare ne.

Cikin fad'a - fad'a yace "damme za ka ce sai gobe result zai fito?".

Murmushi Dr.Abdallah ya yi yace" ranka ya dad'e k'a'ida ne sai anyi hakan, kuma gobe inshaallah zan kawo result d'in kamar yadda ka ke so, a yi min afuwa yallab'ai".

"Okay to nagane ba matsala, sai goben"

Katse wayar ya yi sannan ya kwanta baccin asara.

Hidima a ke ta yi a cikin masarauta dan tun da aka ce Prince Zaid zai dawo kullum cikin hidima ake, yau ne a ke sa ran dawowar su Prince Zaid da Hibbullah, tun safe airport d'in Yemen ya ke cike da magoya bayan prince Zaid, a Polo duk da an hanasu shiga amma k'ofar a cike ta ke da matasa.

Zeenat tun kafin asuba ta tashi, ta sha kwalliyarta, Allah - Allah ta ke a ce a je taron yarima.

'Daukin da ta ke har mamaki ya bawa umman ta, "umma wai da k'arfe nawa jirgin na su zai iso ne?" Zeenat da ta gaji da jira ta ke tambaya.

"Ni ina zan sa ni Zeenat da kin tambayi babanki ai".

Cuno baki gaba ta yi ai kamata ya yi ace tun asuban nan su ka iso saboda Allah". Umma ta ce" tun da har yan zu bai iso ba, ga wanke -wanken cen ki yimin kafin mu je tarb'ar shi".

Dafe k'irji ta yi kamar angayamata abun tashin hankali tace"nashiga uku umma, wana wanke - wanke kuma bayan na gama shiryawa dan Allah ki bari sai mundawo please umma na"

Ta fad'a ta na had'e hannuwanta irin na indiyawa.

Tun wajen goma na safe Dr. Abdallah ya iso cikin masarautar, sai murmushi ya ke ta faman dokawa, iso aka yi masa har cikin falon Fulani ta uku, kowa ya hallara a wajen Lukman,Prince Safwan,Fulani da Fulani ta biyu wato Samira.

Fulani ta uku kuwa,ji ta ke kamar da gaske cikin za'ace ta na da shi.

Sai yatsina ta ke yi,

Likita ya iso fuskar sa tar da murna, "Assalamu Alaikum"

Zubewa ya yi gaban Fulani babba ya d'ibi gaisuwa, sanna ya had'a ya yi wa sauran a tare, hakan da ya yi, ya k'ara rura wutar k'iyayyar ta a zuciyar Samira.

Likita ya gyara coat d'in jikinsa yace"Alhamdulillah sakamakon gwaji ya fito ranka yadad'e"

Farar paper ya zaro daga aljihunsa ya mik'awa Lukman dan a mik'awa mai martaba, idan ya fito. Cikin zak'uwa Lukman ya ce" Doctor (likita) me ya sa me ta ne? "

Mummushi ya yi yace"ranku ya dad'e, ina ta ya ku murna, ai ta na d'auke ne da juna biyu"

Wani murmushi Fulani Hafsa ta yi, yadda planning ya ke tafiya dai dai.

"Alhamdulillah,Allah mungode maka" Fulani babba da farin ciki kwance a fuskarta ta fad'a, mungode da wannan kyakkyawan albishir d'in likita"

Fulani Samira kuwa kallon likitan kawai ta ke yi ta na mamakin cikin da Hafsat d'in ta ke da shi, daure kishin da ya taso mata ta yi tace, "mashaallah muna ta ya ki murna, Allah ya inganta, likita akwai kyauta da za ta zo yan zu daga gareni"

Zubewa k'asa likita ya yi ya na ta godiya kamar ya aro baki.

Prince Safwan kuwa cewa ya ke"ni zan fara yiwa mai martaba albishir d'in nan" Lukman ma cikin farin ciki yace "tab ka ma isa, ni ne zan fara yi masa wannan albishir d'in ai"

Gaba d'aya su, su ka yi murmushi. Fatan alkhairi su ka yi mata sannan su ka tashi kowa ta koma part d'in ta.

Likita na shiga office d'in sa ya ji alert ya shigo 10 millions sun fad'a

Hannun sa har rawa ya ke ya d'auko ya duba. "Wow ni ne da wannan kud'in wayyo arziki na ya zo, dare d'aya Allah kanyi bature, bari in sanar da yallab'ai sun shigo".

Kiran Lukman ya shiga yi,amma ba'a d'aga ba,hak'ura ya yi anjima ya k'ara kira, amma kafin nan text (sak'o) ya tura ma sa ta wayar ya Samar da shi kud'in ya shigo, sannan ya rufe office d'in ya fice daga asibitin gaba d'aya.

Lukman ne zaune gaban mai martaba ya mik'a masa result ya na ta murmushi, " Allah ya k'ara lafiya da nisan kwana likita ya zo d'azun, ya kawo sakamakon".

"To mashaallah" ya fad'a ya na karb'ar takardar da Lukman ya mik'a masa.

Bud'ewa ya yi ya fara karanta wa da kansa tun da a cikin turakarsa ne, ganin abin da sakamakon ya nuna ne ya sa sarki y.....

Hamza da tawagar 'yan JIHAD DA'AWAH FOUNDATION, su ka sauka a kasar Morocco, domin d'aukaka kalmar Allah. Sun sauka a bayan wani gari Wanda su ke rayuwa kamar dabbobi, ba su da wani addini haka nan su ke rayuwa.

Sultana ce gaban mahaifiyarta kuka ta ke kamar ranta zai fita "mommy ki sa daddy ya gayawa sheik Usman ni Sudees na ke so na aura, idan ba haka ba Wallahi sai na shiga duniya" shiru mommyn na ta tayi ta rasa meyasa Sultana ta nace sai wannan ustaz d'in ta ke so, ga ta da masoya tun daga 'ya'yan sarakuna da masu muk'amai manyan mutane dai,amma duk tak'i sai ita sai Sudees.

"Sultana ni bazan iya wannan abun naki ba, ki je ki same shi da kan ki,ki gayamasa ni nagaji da ganin wannan yaron ya na wulak'anta ki. ke kad'ai Allah ya ba mu, idan mijinki ne Wallahi dole sai ya aure ki,komai girman kansa, sai ya yi miki biyayya kuwa.

"Sultana ba abinda za ki nema, a duniyan nan ban yi miki shi ba Wallahi Tallahi sai kin mallaki yaron nan a hannunki dan ubansa" ambassador.....,

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: _□□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

TSARAWA DA RUBUTAWA

NA

R.HUSSAIN DA NOORY

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

*⚜©J.A.W*_

LITTAFIN *KUDI* *NE* *KIBIYA KI* *KARANTA BA* *TARE DA CIN* *HAK'K'IN WA NI* *BA*

NORMAL GROUP N300

V I P N500,

DOMIN K'ARIN BAYANI KU TUNTUBEMU TA WANNAN LAMBA 08107916039.

.....murk'ususu ta ke kamar gaske"wayyo ciki na,innalillahi wa'inna'ilaihirrajiun wayyo zan mutu" Fulani Hafsat ke ta burgima akan k'aton gadon ta.

Jakadiya da ke kusa da ita duk ta gigice kira ta ke "lahaula wa'la k'uwata illah billahil oh ni Lami na ga ikon Allah".

Da sauri baiwarta ta ta fita don ta sanar da sallama ya je fada ya sanar wa da mai martaba halin da ake ciki.

Lukman da dawowarsa kenan da ga wajen likitan su mak'udan kud'i ya shak'a ma sa ya tsara masa irin result d'in da ya ke so a bawa Fulani ta uku idan ya zo duba ta.

Dr.Abdallah Yasir Tun da ya ga Lukman wajen k'arfe takwas na dare ya san ba lafiya ba.

Tashi ya yi cikin girmamawa ya ce " ranka ya dad'e yariman Sudan Allah ya k'ara lafiya da ka kira ni ma ai da ba sai ka zo ba".

Lukman da ya zauna ya k'ara had'e rai cewa ya yi" ba wani abu ba ne ya kawo ni,na zo ne Dan akwai wani aiki da za kayi mana, mai sauk'i ne a wajen ka amma rashin yin sa zai ja maka had'ari a rayuwar ka" gaban Dr.Abdallah ne ya fad'i nan da nan gumi ya fara karyo masa duk da ACn da ke cikin office d'in na sa.

Cikin rawar murya yace"ranka ya dad'e me kake so?"

Murmushin mugunta Lukman ya yi ya na d'aga kan sa sama, ya na shafa gemon sa da hannunsa sannan yace" Aunty na ce ba tada lafiya, ina so idan ankira ka ka tabbatar da cewa ta na d'auke ne da ciki a jikin ta".

Ajiyar zuciya doctor ya sauke ya yi murmushi ya na cije bakin sa dan yasan ba k'aramin alkhairi zai sa mu ba idan ya aikata hakan.

"Hmmm ranka ya dad'e dan wannan ai mai sauk'i ne, ba damuwa"

Lukman da yasan za'a rina dan sai da ya bunciki halin Dr.Abdallah ya gano mutum ne mai son kud'in tsiya, har abortion(zubar da ciki) ya ke wa 'yanmata a asibitinsa.

Sannan ya kawo masa ta yin wannan Dill (harkar). "Yauwa likita ba ni account number d'in ka, ka na aikatawa za kaji alert na 10millions". Kafin nan ga wannan zaro rafar dubu dubu ya yi har guda buyar a aljihun alkibbar sa, dubu d'ari biyar ya ba shi cash.

Dr.da ya ji kud'i sai godiya ya ke ya ba ba wa Lukman account number d'in nasa. Sannan Lukman ya dawo ya na jiran ya ji auntyn ta fara rashin lafiya.

Ganin baiwar ta, ta fito daga part d'in auntyn ya sa ya yi murmushi dan ya san komai ya na tafiya dai - dai, da sauri ya wuce part d'in sa dan ya san za'a nemeshi a matsayin sa na d'a agareta. Sadiya baiwar da ta zo ta gayawa sarki abin da ke faruwa ta na shiga fadar zubewa ta yi bakin k'ofa ta na nishi da k'ar ta ke magana.

Sallama ne ya ce" me ke tafe da ke baiwa?"

"Fulani ta uku ce ba lafiya,ta na kwance a d'aki ba ta san in da kanta ya ke ba"

Ta na gama bayani sallama ya dubi mai martaba dan ya ji me zaice.

Sarki Abdurtahman ya ce" subhanallah, a kira likita ya zo da sauri" a take aka kira Dr.Abdallah Wanda ya ke jiran kiran tun d'azu, ya na gani ya d'auka da sauri dan yasan sarkin iso ne ya k'ira shi dan in dai kira daga fada ne to tabbas sarkin iso ne me wannan damar.

Da sallama ya d'auka daga can masarautar aka sanar da shi abun da ya dad'e da sanin sa, cikin nuna tashin hankali ya ce"okay okay gani nan zuwa yan zu"

Ya shirya komai na

 sa a briefcase ya wuce zuwa masarautar.

Part d'in Fulani ta uku ya shige ganin su Lukman da mai martaba ne kawai a d'akin ya sa Dr.Abdallah zu be wa dan Isar da gaisuwa ga mai martaba, cikin sauri sarki Abdurrahman ya ce" yi aikin ka likita".

Tunda ya ga yadda Fulani ta ke ya fuskanci makirci ne dan ga idanunta farare tes kuma wai kukun jin jiki ta ke,haka ya ce "sannu Allah ya k'ara miki lafiya me ke miki ciwo?"

Cikin muryar jin jiki da numfarfashi ta ce "ci...cik....ciki na doctor wayyo zan mutu" k'ara sassank'amewa ta ke.

Wata allura ya d'auko ta tetanus ya yi mata,Sannan ya d'aura mata ruwa ya zuba allurar paracetamol aciki da wacce za ta sa ta yi bacci ya yi mata,sannan ya d'auki sample d'in jininta.

Juyowa ya yi wajen su Lukman wanda ya yi wujiga - wujiga kamar gaske ya ce" ranka ya dad'e ba wani ciwo ba ne mai tsanani,yan zu dai zanje lab a duba a ga me yake damunta, zuwa gobe da safe zan kawo result d'in inshaallah "

"Wannan wacce irin maganar banza ce, result d'in ne sai munjira har zuwa gobe?" Lukman ya fad'a cikin jin haushi.

Mai martaba da ya ke kan kujera a zaune yace" ya isa haka Lukman"

Dr.Abdallah ne cikin kwarewar aiki ya ce"Allah ya taimake ka, dole sai anyi gwaje - gwaje ne kuma ya na d'aukan lokaci kafin sakamakon ya fito, yan zu sha d'aya ta gota idan na ce zan dawo a yan zu ba zai yuyu a gama gwajin yadda ya kamata ba".

Cikin gamsuwa da bayanin sa mai martaba ya ce"Allah ya kai mu goben da rai da lafiya"

"Amsawa su ka yi da " amin" sannan likita ya yi musu sallama ya tafi.

Jakadiya da ta lab'e ta najin komai, girgiza kai ta ke ta na mamakin makirci irin na larabawa cewa ta ke" yau naga ubana a rashin jin tsoron Allah" jin motsi ya sa tai saurin lab'ewa daga gefen d'akin.

Likita na fitowa Fulani babba na tawo wa dan ba tasaniba sai daga baya Saff ya ke gayamata.

Lokacin da likita ya wuce Jakadiya ta fito kenan ta dawo jikin k'ofa Fulani ta da kuyangarta ta sawo kai.....

Lantan ce ta shigo dan yan zu ta komai yarinya ba ta san komai ba tun da Bisi ya daketa shikenan ajiyar zuciya Rona ta sauke "kai Lantan K'ainani ya ba ki sauk'i dai" Rona ta fad'a.

Hantsi da take had'a walkin da Lu'u zai sa gobe ta ce "Rona idan kun je gurin bauta ki cewa K'ainani ya ba mu irin Bisi domin kariya ne a wajen mu".

Shiru Rona ta yi tana tunanin maganar Hantsi dan ita tun da ta ke ba ta tab'a tunanin haka ba.

Lamma ce ta ce" Hantsi wa ni Bisin za'a k'aramana bayan wanda k'ainani ya turo mana?"

Bisi da tun d'azu ya shigo murmushi kawai ya ke daman Hantsi ta na sane da shi amma bata tab'a yi masa magana ba?

Ganin sa suka yi kawai a d'akin, "Rona ce tace" Bisi baka je shagalin ba ne?".

"Eh amma yan zu zan je, damantsan sa kawai Hantsi ta kallah ta sun kuyar da kai, fata ta ke k'ainani ya sa baiji abin da ta ke fad'a ba. Shi da Rona ne su ka tafi wajen shagali.

kurciya tai ta aman wuta cikin firgici boka 'Dundumi yace" a'a ba zan tab'a bari su zo mana masarautar mu ba, sau biyu su na hallakamin ma'aikata na, na rantse da K'ainani sai na hallaka su".

Ihu ya ke ya na surutan tsafi wata kunfa ce Ke fita ta bakin sa da hancin sa, mesa ce k'atuwa ta b'ullo idonanunta kamar fitila tsabar haske, gaba d'aya mutanen da ke d'akin Hazid d'in sai da suka razana da ganin ta. Hazid ne ya dawo hayyacin sa ya ga mahaifiyarsa cikin keji, ganin sa cikin sark'a ya sa ya yi ihu ya na "Ku kwance ni na rantse duk wanda ya yi wa Shiwu haka sai na hallaka shi".

Sarki Gannami ya ce " Hazid ba ka ga mesa ba ne" Hazid da bai kula da ita ba sai yan zu,ya sa ya tsaya ya na kallon ta,tun da ya ke bai tab'a ganin mesa me girman ta ba, duk da ba dukkan ta tafito ba daga k'asan, kan ta ne kawai sai kad'an daga sassan jikin ta, umarnin boka kawai ta ke jira.

Boka 'Dandumi da ya ga kowa ya sallama masa ya sa ya ji tabbas shi zai mulki duk kan masarautar ba ma ita kad'ai ba har duniyar ma baki d'aya.....

Turk'ashi.

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

TSARAWA DA RUBUTAWA

NA

R.HUSSAIN DA NOORY

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.W.A

SADAUKARWA GA MASOYAN MU □

LITTAFIN KU'DI *NE , KI BIYA KI* *KARANTA* *CIKIN AMINCI*

NORMAL *GROUP N300*

VIP N500

Domin k'arayin bayani ki tuntub'emu ta wannan number 09107916039.

FREE PAGES YA KUSA K'AREWA

.....✍ Boka Gannami yace wa mesar nan "zan aike ki wajen wasu mutane, na aiki bayi na har biyu ma su had'ari amma sun gagaresu, nasan ke za ki iya hallakamin su ki je ki nemosu duk in da su ke a fad'in duniyar nan ki hallakamin su, barin su na iya zama had'ari ga MASARAUTAR MU, da rayuwar mu gaba d'aya" ta ke mesar ta bud'e bakinta wani ruwa mai zafi ta ke fesarwa, wan da in dai ya tab'a mutum ko dabba sai ya k'one. Ta ke ta nitse cikin k'asa ta b'ace.

Hazid ne ya ce "ya shugaban bokaye, su waye wannan mutanen da ka ke tsoron shugowarsu MASARAUTAR MU?"

Sarki Gannami yace" Hazid boka 'Daundumi ya ce su na da hatsari sosai, ni da kaina na so ya barsu su shigo, mu ba wa K'ainina jinin su, ko da sun kai girman runduna na wa amma yace ba su da yawa sai dai k'arfin wani abu da ke tare da su, wan da ba tsafi ba ne".

Hazid ya bushe da dariya yace " hahhh hahhhh amma boka 'Dundumi ka ban kunya akan wasu tsirarun mutane ka aika musu, wannan mesar ai kuwa ka ban kunya"

Boka 'Dundumi yace" ya shugaba na nayi - nayi na gane lagunsu amma abun yacitura,tabbas in dai ban dakatar da zuwan su wannan MASARAUTAR ba to kuwa mulkin kuma sai ya k'are".

Takobi Hazid ya zare ya na nufo boka 'Dundumi ya na cewa "k'arya ne boka ina rantsuwa da k'arfin tsafin baba na ba wanda ya isa ya karya mana MASARAUTAR MU zan so su zo, kuga yadda zan musu kisan gillah da kaifin takobina".

Boka 'Dundumi ya bushe da dariya me firgitarwa cikin muryar yara yace" Yarima tun da k'arfin tsafina bai nunamin abin da su ke tak'ama da shi ba to kuwa na rantse da girman K'ainina ba mahaluk'in da ya isa ya gani, nasara d'aya da za ka samu shine su na da maganin da zai warkar da kai kuma warkar da kai dai - dai ya ke da karyewar MASARAUTAR MU kuma na yi alk'awarin ni da kaina zan samo maganin da za ka warke".

Hazid ne yace " k'arya ka ke tsoho, ni da kai na nasan yadda zan yi da su, tun da kai ka kasa"

Sarki Gannami da ya gaji da wannan zancen na su yace" Hazid zaka warke tabbas nasan K'ainani zai warkar da kai ka k'yale zancen boka 'Dundumi ni nasan k'arya ya ke". Boka da ya ke murmushin mugunta ya na sak'a musu mugun nufi a ransa, yadda su ke k'aryata shi a yanzu, ya san duk abin da ya fad'a musu to kuwa sai ya tabbata amma sun manta da waye 'Dundumi akan buk'atar kansu.

Shiwu da ta ke cikin keji ta na jin abin da su ke fad'a ta ce"ni nasan Hazid zai warke ya shugabana ka fitar da ni daga cikin kejin nan dan furfurar kan kakanka Hauno na tuba ya shugaba"

Sarki Gannami ya ce "tun da ki ke son ganin bayan MASARAUTAR MU anan za ki ta zama Shiwu". Hazid yace " Ya babana, kar ka manta uwace a gare ni, in dai ana son ayi bikin shekara cikin albarkar K'ainina to ka kwance Shiwu idan ba haka ba zanyi b'arnar da kowa sai ta ja masa tsinuwar K'ainina.

Sanin halin Hazid ya sa sarki Gannami nu na kejin da sandar sarautarsa ta ke kejin ya b'ace Shiwu ta fito, rungume d'an nata Hazid ta yi ta na masa kirarin da ta ke masa acikin kunnensa, soyayyar d'a da uwa sai Allah.

Obi ganin anfito da Shiwu ya sa ta je fa mata wa ni abu kamar k'onar wuta da idon ta, kafin abin ya je ga jikin Shiwu,Hazid ya rik'e shi ido kawai ya k'urawa Obi, ta ke jikin ta ya fara rawa, dan tasan waye Hazid ya sha Jamata kunne akan Shiwu amma ba ta ji. Je fa tsafin ya yi a jikin Obi ta ke ta hau ihu ta na rok'on Hazid, boka da ya ga abin da ya ke faruwa ya sa ya bushe da dariya yace "ba'abin da ke sa in nishad'i irin rama cuta ga macuci ka yi dai - dai yarima Hazid"

Take jikin Obi ya yi burd'in - burd'in kamar k'una, sai d'aukan ta akai,aka mai da ita d'aki, sai ihu ta ke tasan tun da Hazid ya rama to kuwa ba zai warkar da ita ta dad'in rai ba.

Yau ne bikin shekara kowa ya sha ado cikin sabon walkinsa, mata sai tuk'a tuwon accan su suke, domin ci da miyar naman hadaya.

Rona ce ta fito cikin shirinta Lamma na cewa" Rona ki tawo mana da miyar hadaya ko K'ainina ya ba mu daman fita kamar kowa".

Bisi ne ya shigo cikin sabon walkinsa,dogon mutum k'akk'arfa damtsen hannunsa d'aure da guru kalar walkinsa fuskar sa d'auke da murmushi

Jikinsa luf - luf kamar ba mai sana'ar faskara ice ba.

Hantsi ce ta fara ganin shigowarsa d'akin, Lu'u da ya fito shima cikin shirinsa na janwalki, ganin Bisi a gidansa ya razanar da shi,dan bai tab'a sanin yana zuwa gidan ba, tsoron tonuwar asirinsu ne ya sa yace" Samari lafiya?"

Bisi ya sakar masa murmushi sannan yace "lafiya lau,na zo ne in ga su Lamma kafin in tafi wajen bauta".

Lu'u cikin razani yace" anan g....

Rona ce ta katse shi da cewa"Bisi shigo mana yan zu nake tunanin ko ka wuce wajen bauta"

Lu'u da mamakin ya akayi su ka san shi ya kamashi. Lu'u yace "Rona waye wannan?" Bayani tai masa sannan shi ma ya ji hankalinsa ya nutsu da Bisi.

Haka su ka tafi wajen bauta a tare akabar su Hantsi da Lamma a d'akin su duk gari an tafi wajen bauta.

Cike wajen bautar ya ke da mutanen garin Duhuwa ga hadaya an rataye su a jikin dogon gini, wani k'aton mutum ne rik'e da mashi Wanda za'a tsire hadaya K'ainina ya sha jini,sannan a yanka a yi miyar shekara da namansu.

Bisi da ya ke jin rashin dad'i a ransa ganin za'a yanka hadaya haka zuciyarsa ta ke jin, wannan ba dai - dai ba ne, ba yan da zaiyi haka shima ya kama rawar da suke yi a wajen ya na tayasu farin ciki.

Fitowar sarkin Gannami da Hazid da Shiwu ne yasa kowa ya nutsu a ka hau gaisuwa sarki Gannami na hard'e akan kujerar azurfa wa su bayi sun d'auko shi akan kafad'arsu.

Haka Hazid da Shiwu duk d'auko su a ka yi.

Bayan angama rawa da gaisuwa aka tsire hadaya k'ok'on tsafi a ka Tara a ka yanka su jinin ya taru a k'ok'on boka 'Dundumi ne ya ke tsafin sa ta ke jinin ya b'ace ihu gaba d'aya gurin ake ambawa K'ainina jini. Naman a ka yanka wuta sosai a ka hura, ana ta miyar da kowa a hannu ake ba shi domin samun albarka, samarin gurin sai neman matar da zasu aura su ke, dan duk shekara ake aure a wajen,in dai ki ka bari saurayi ya rike ki to shikenan kin zama matarsa.

Bisi na gefe a tsaye abokan sa matasa ne su ka zo su ka ce "Bisi ka zo muje samo mata a wajen

Layin 'yanmata mana".

Yatsina fuska ya yi yace" Ni ba aure zanyi ba ku je ku kuyi"

Timi ne yace"ba na gaya muku ba, baisan me ya ke masa ciwo ba"

Haka su ka bar shi su ka tafi.

Hazid neman budurwarsa ta madubi kawai ya ke,amma ba ita haka ya ji bayason kama ko wacce mace a wajen dan budurwar kawai ya ke buk'ata, sarki Gannami ya ga k'asa ta na girgiza ta na t.....

* * * *

Misalin k'arfe 12:45 jirgin Prince Zaid da Hibbullah ya sauka, dogarai da fadawa ne kawai su ke kai kawo a airport d'in, matasa kuwa sai ihu da murnar dawowar fitaccen d'an wasan Polo kuma Prince d'in su Zaid Abdurrahman Abdul'azeez su ke.

Fitowa ya yi sanye da kayan sarauta bak'ar alkibba ce a jikinsa da glass bak'i Wanda ya b'oye ainahin idanunsa. Tun da ya fito ake ta faman d'aukar sa a camera ko ta ina, sai ka re shi ake yi ana ba shi tsaro, Hibbu na gefensa cikin shigar coat brown ya sha stoking.

Mota aka bud'e masa sabuwa dal musamman mai martaba ya tanadeta saboda dawowarsu Prince Zaid da Hibbullahi Waziri Usman.

Mai martaba ya na ganin abin da result ya nu na ya yi farin ciki dan ba k'aramin tausayi Fulani Hafsa ta ke ba shi ba, ganin ita Allah bai bata haihuwa ba, a ta ke yace wa Lukman "an bawa Likita kujerar Hajji guda uku saboda wannan kyakkyawan result d'in.

Lukman ya saki murmushin gefen baki yace" godiya ya ke ranka ya dad'e,Allah ya sa a gama lafiya".

Mai martaba ya amsa da "Amin Lukman.

Me ka ke so na baka a matsayin tukwici?"

Murmushi Lukman ya yi yace"ba abin da na ke so, komai ina samu raka ya dad'e".

Fitowa ya yi yana fito dan nasara kawai ya ke gani cikin kwanciyar hankali. Jakadiya ya gani ta na kallonsa ta na dariya,zuwa ta yi tace"ranka ya dad'e "Alhamdulillah yarima babba ya iso lafiya,su na hanya yan zu haka".

Da sauri Lukman ya ce "dama yau ne ko, okay ai namanta shap da ni da kai na zan d'akko abokina kuma d'an uwana ai,amma yan zu ma ba ta b'aci ba"

Jakadiya cikin bugar cikinsa tace"ranka ya dad'e ina ta ya ka murna,Fulani an samu rabo, Allah ya inganta, fatan mu samu takwaye" kallonsa ta yi ko ya zai yi, fito ya ci gaba dayi ya wuce part d'in Auntyn na sa, dan sanar da ita kyautar da akayiwa likita.

Shigar sa d'akin kenan ya same ta a.....

Littafin kud'i ne, ki biya ki karanta cikin aminci.

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

TSARAWA DA RUBUTAWA

NA

R.HUSSAIN DA NOORY

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

⚜©J.W.A

SADAUKARWA GA MASOYAN MU

PAID BOOK

NORMAL GROUP N300

VIP N500

For more information WhatsApp 08107916039/ 08145498489.

.....✍k'asa ce ta tsage ta ke mesar nan ta bayyana gaba d'ayanta,ihu 'yan garin Duhuwa su ke su na matsawa. Boka 'Dundumi ne cikin tsoron me tazo ma sa da shi ya tsaya dai dai kan mesar ya na surutai ta ke mesa ta fara feshin ruwan zafi can ta tsaya sannan , boka 'Dundumi ya shek'e da dariya ya na yabawa mesar tsafin sa, da tazo masa da bayanin mutane shida duk da ba yadda ya so ba ne, ko ba komai ya san sunan k'asa su Nigeria da sunan garinsu Kano daga haka ba ta san komai akan su ba.

Cikin jindad'in samun nasara dan yanzu ya san k'asar da samarin su ke,duk da bai tab'a jin sunan ta ba,amma ya rik'e duk wanda ya shiga MASARAUTAR DUHUWA in dai d'an Nigeria ne sai sun ninka irin kisan gillar da su ke wa bak'i a kan sa.

Take mesa ta nitse cikin k'asa ta b'ace gurin ya shafe yadda ya ke, boka 'Dundumi ya matsa wajen sarki Gannami yace"ya shugabana, K'ainani ya ji dad'in hadayar yau jinin samarin mai albarka ne, tun da gashi ya ba mu sa'ar sanin mak'iyan da su ke son ganin bayan MASARAUTAR MU, duk da ba sanin su mukayi ba,amma mungano k'asar su da garin da su ke a duniya".

"Hahhhh hahhhh K'ainina K'ainina"

sarki Gannami ya fad'a. Take 'yangari su ka d'auka da cewa K'ainina!!!!!

sarki Gannami cikin jindad'in nasarar da su ka fara samu yace" ya ku mutanen Duhuwa K'ainina ya karb'i hadayan mu, ya bamu nasara akan abun da ya gagari shugaban bokayen duniya" gaba d'aya wajen Ihu su ka rud'e da shi su ka cika da murna kowa ya na farin ciki.

Aure su ka dinga yi a wajen domin samun nasara,tun da K'ainina ya karb'i hadaya duk samarin wajen sun samo mata, sai kad'an wad'an da sai wata shekarar za suyi suma saboda ba su yi fansar hadaya ba da 'yanmata da tu ni sunyi auren suma, ciki kuwa har da Bisi da shi ba wannan tsarin a rayuwarsa.

Haka a ka sauke miyar naman hadaya a ka raba layi layi ake bin ana zu ba wa kowa idan da dan abun zuba wanka ka zo haka za'a tarfa maka aciki, idan babu kuwa a hannu za'a zuba maka, kan Bisi a ka zo hannu ya sa a ka zuba masa kallon miyar ya ke kamar kullum tun yana k'arami baya ci, saboda ya na da tsantsani sosai ko abincinsu ba'a ko'ina ya ke iya zama ya ci ba.

Timi da yasan halin Bisi k'asa - k'asa yace" Bisi ina jiye maka,ranar da K'ainina zai la'anceka, duk wani abu na al'ada kai ba kaso, meyasa?"

Bisi ya amsa shima k'asa - k'asa "nima bansaniba, kawai inajin hakan ne a raina banason al'adarnan kuma K'ainina ba zai tab'a gane ni ba ni nasani".

Angwaye da amare kawai aka bari awajen bauta saboda neman albarkar aure, dole ka ajiye matar da ka aura bok'a 'Dundumi ya fara sa mata albarka, sannan idan ya

gama sai kaje ka d'auke ta ka kai gidanku, shikenan ka yi aure sai ka canza walki, daga bak'i zuwa ja,matar ma haka.

Sai da boka 'Dundumi ya yi sati ya na sawa amare albarka sannan ya gama kowa ya d'auki matarsa.

Halwar tsafi ya shiga ya na bunciken matasan da su ke tsoratar da shi, dan tabbas ganin zuwansu ya ke,babbar matsala yaushe ne zuwan,ta ina zasu b'ullo?

Bisi da Lamma ne zaune a d'akin su Hantsi, sun yi sabo sosai dan idan bai zo ba har cigiyarsa ta ke, yakan yawan sako Hantsi a hirar da su ke da Lamma, amma ba ta tankamasa, sai sun gama hirarsu ya fita sannan za tai tayiwa Lamma zancen ai Bisi ka za, Bisi ya yi ka za, yanzu Lu'u ma ya sake sosai da Bisi har ya na tunanin nan gaba ya aura masa duk ka 'ya'yan nasa biyu Lamma da Hantsi ta hanyar kai su wajen bauta,ba tare da barin kowa ya sa ni ba, son Bisi ya ke ganin bashida hayaniya kuma ya na da hankali, amma ta ina zai fara wannan kasadar,zuwa wajen bauta ba tare da neman izini ba babbar matsala ce dan za'a iya tsire shi saboda cin amanar

MASARAUTAR ne.

* * * *

Bayi ne sunyi sahu sahu tun da ga bakin garin na mu har zuwa cikin MASARAUTAR MU kowa fuskar sa d'auke da farin ciki zai ga yarima Zaid Wanda ya kwashe shekaru bakwai bai zo ba, Zeenat ce cikin k'awayenta kowa sanye ya ke da kayansu na bayi,bak'i da kore, sun yi farrrr ana jiran isowar yarima.

Had'addiyar helux ce tasha tin tieck ce ta shigo MASARAUTAR sai kid'e kid'e da bushe - Bushe ke ta shi, da sauri a ka bud'e masa k'ofa dan ganin dubban jama'an cikin MASARAUTAR da kowa jiran ganin Prince Zaid ya ke, k'afarsa ya fara sa kowa ya fi k'arfin minti biyar kafin ya ciro d'ayar ya fito.

Zeenat da ta matsu ta ganshi ganin yadda ya ke delaying kamar bayason fitowa ya sa taja shaki"mtswww aikin banza,dan ya ga ma andamu da ganins.... Kafin ta k'arasa mitar ya fito kirari aka shiga yi ma sa"Takawarka lafiya yarima mai jiran gado,barka da zuwa d'awisu sarkin ado, gyara kintsi da kyau, toron gwiwa dan sarki jikan sarki" ko ta ina kirari da bushe bushe ke ta shi.

Zeenat na ganinsa ta ce "kai amma naji kunya Wallahi,Ashe ma kama da larabawa ya ke,ba ma wani kyau ne da shi ba,daga ganinsa akwai girman kan tsiya, to ba laifi dai"

Haka ta ke ta cewa,kuma ta na binsa da kallo har ya shiga cikin fadar.

Lukman da ya yi wani irin tsallen murna ya rungume abokin nasa Prince Zaid yana cewa" my Bros I miss you a lot ,I can't live with out you in my side" hawayen farinciki kawai Lukman ya ke ya k'ank'ame Prince ya hana ma Prince Safwan ya rungumeshi, Fulani babba sai k'ara k'aunar Lukman ta ke ji a ranta yadda ya ke bala'in k'aunar yarima,addu'a ta ke musu Allah ya barsu tare, sai da ya d'an dad'e sannan ya sake shi.

Prince safwan ne ya rungumeshi ya na cewa"welcome my bros fatan ka dawo lafiya?"

Prince Zaid da farin cikin ganin shi cikin ahalinsa yace"Normal saff ya gida?"

"K'alau" ya amsa masa.

Mai martaba ne da yagaji yace"to a barshi mana mu ma muji d'uminsa ko"

Darawa sukayi amma banda Fulani ta biyu Samira kenan,hakan ma wani bak'in ciki ne ya rufeta,ta rasa ya zatayi da Zaid d'in nan,ta so a kashe shi kafin ya shigo MASARAUTAR amma ina, Jakadiya kuma ta tabbatar mata da cewa boka yace ya na ratsa bakin gate d'in zai fad'i ko shurawa ba zai yi ba,amma ga shi nan k'alau da shi. Dole ta sake shiru.

Fulani Hafsat kuwa da ke yau ne aka tabbatar da ita a matsayin maiciki, d'an mik'ewa ta yi,ta k'araso kusa da Prince Zaid d'in cikin fuskar makirci, da nuna k'auna kamar yadda Lukman ya ke sanar da ita, salon yaudara kala - kala ta ce"barka da zuwa yarima Zaid,munyi kewar ka sosai fatan ka dawo kenan ko?".

Cikin jindad'in yadda dangin sa suke k'aunar sa yace"mami na nima nayi kewarku sosai,fatan na sameku lafiya?"

"Lafiya lau" ta amsa.

Sauran k'annen sa ne su ka yi masa barka da dawowa, duk wannan had'uwar sarki Abdurrahman ne ya sa duk su had'u a sashensa don kar ya sha wahalar bin part - part daga dawowarsa,idan ya so in ya huta zuwa gobe sai ya je part d'in kowa.

Mahaifiyarsa Fulani babba ta na zaune ya k'ara so jikinta ya shige ya na rungumeta"my first love I really miss you"

Murmushi kwance a fuskarta ganin d'annata cikin k'oshin lafiya da kuzari "ta ce mu ma munyi kewarsu Zaidul'abideen ya England"

"Alhamdulillah koma lafiya lau mommy na".

Haka su ka gaisa da kowa daki daki sanna Hibbullah da Mahaifinsa waziri Usman su ka nufi gidansu.

Princess Bilkisu ce ta ci ado sosai domin zuwa tarar abin sonta Prince Zaid, sai dai kash ba ta s.....

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: _□□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

TSARAWA DA RUBUTAWA

NA

R.HUSSAIN DA NOORY

□□

JARUMAI WRITER'S ASSOCIATION□

{Marubuta masu aiki da jarumta domin wa'azantawa ilimantarwa, nishad'antarwa tare da fad'akarwa da jama'a bisa harshen hausa}

https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=337435884671992&id=103920888023494&sfnsn=mo

*⚜©J.A.W*_

LITTAFIN *KUDI* *NE* *KIBIYA KI* *KARANTA BA* *TARE DA CIN* *HAK'K'IN WA NI* *BA*

NORMAL GROUP N300

V I P N500,

DOMIN K'ARIN BAYANI KU TUNTUBEMU TA WANNAN LAMBA 08107916039.

*Albishirinku jama'a, shin ko kunada labarin *NOORY DATA SERVICES*? To ku matso kuji, ana saida data akan farashi me sauki, kuma gashi da 'karko😍.

500mb□□150, 1gb□□250, 2gb□□500, 3gb□□750, 4gb□□1000, 5gb□□1250, 6gb□□ 1500.kuji arha jama'a□□□□□..*for more info call/chat 08145498489*

.....✍Ha da ha dan tafiya kawai Hibbullah ya ke burin sa su isa gida lafiya shi da Prince Zaid, jin wayarsa na k'ara alamar kira ya sa shi tsayawa a cikin airport d'in d'auka ya yi da fad'in "Hello Prince Saff" daga can gida Niger kuwa Safwan ne ya mik'awa Bilkisu wayar, da rawar jiki ta amsa.

Da ke a hands free ya sa wayar shiyasa ta ajiye ta akan cinyar ta"Hello yaya Hibbu ya jikin Prince d'in?".

Jin muryar k'anwarsa Bilkisu yasa ya ce "ya samu sauk'i ai,ba ki ji labarin ba ne,kin zo kin d'aga wa Mommy hankali ko".

Bilkisu ce ta ce" a'a mun k'ira Prince munji bai d'auka ba" sai hawaye sharrrrr.

Hibbullah da yasan halin Prince d'in yasan k'alau ya ke sarautar ce kawai ta tashi, shiyasa yak'i d'aukar wayar.

Ce mata yayi"okay yan zu ba ma tare da shi, amma anjima zan had'aku inshaallah "

Cikin raunin jiki ta ce "to yaya Hibbu sai anjiman".

Kashe wayar ta yi ta mik'awa Prince Saff shi kuma ganin yadda Bilkisu ta damu da Prince ya sa ya ke jin tausayin ta,dan ya san waye Prince Zaid.

Fulani ce ta ce" Bilkisu kin dai ji da kan ki ko,ya samu lafiya tun a jiyan ma, yan zu ki kwanatar da hankalin ki nan da sati biyu,inshaallah za su ma dawo kinji?"

"To Mommy nagode " Bilkisu ta fad'a ta na mai tashi ta yi musu sallama dan ta koma gidan su.

Bilkisu na fitowa ta hango wasu 'yanmata tsaye da alama bayi ne,biyu sanye su ke da uniform d'in islamiyya d'ayar kuwa atamfa ce jikin ta Zeenat kenan.

Tun da Bilkisu ta d'ora ido akan Zeenat taji ba ta sonta, haka kawai hassada da bak'incikin Kyan da yarinyar ta ke da shi ne ya kamata. Haka ta wuce da baiwar ta su ka nufi mota dan komawa gidan mahaifinta waziri.

Wacece Bilkisu????

Bilkisu 'ya ce ga Waziri Usman Hikima ita kad'ai ce 'ya mace a gurin iyayen ta waziri da Hajiya Amina.

Ta yi karatun ta har matsayin digree a k'asar Egypt, in da ta karanci computer science.

Bilkisu ita kenan k'anwa ga Hibbullah Wanda ya ba ta shekara uku cis tsakanin su.

Sun ta so tare da Prince Zaid da Saff kasan cewar su a masarauta d'aya. Tun su na k'anana Bilkisu ta san so dan tun da su Prince Zaid su ka bar k'asar ta gane Ashe ba shak'uwa ce tsakanin ta da Prince Zaid ba, son sa take iya rayuwa da mutuwa.

Bilkisu ta na da wani banzan hali na wulak'anci da izza akwai ji ji da kai ko su Fiddausi da su Ke jinin sarki Abdurrahman Abdul'azeez ba su kai ta jin mulki ba.

Yan zu haka ta koyo d'abi'un turawa duk in da tacecceyar Mara kunya ta ke Bilkisu ta shafe su.

Tun ta na Egypt karatu ta ke da son rayuwar turawa yan zu haka ta na da wani saurayi bature mai suna John, ba aure su ka yi ba.Amma rayuwa su ke tamkar mata da miji. Duk san da ya so ganin ta k'asar ya kewa tsinkaye ita kuma za ta sauke shi a masarautar mu.

Kasan cewar d'an ambassador ne shiyasa ba wan da ya gane masha'arsu su, su ke ko wa ya d'auka shak'uwa ce irin ta yan makaranta.

Son da ta kewa prince so ne na aure,kuma ta na ganin ko me za'ayi sai ta aure shi, kuma ba za ta rabu da john ba. Gaba d'aya ba ta in da ta d'akko halin Hibbullah ko iyayensu dan su mutanen kirki ne.

Giyar mulki ta sa har syrup da shisha da k'waya ta ke afawa, idan kuwa john ya zo,ko ita ta je to kuwa kwana su ke aikata tsiya wannan kenan.

* * * *

Wasu manya - many an maza ne su ke rik'e da wasu 'yan samari gida biyu, an d'aure su da igiya ana jansu kamar tumaki,dayan ba zai fi shekara ashirin da rakwas zuwa da tara ba,dayan kuma baifi shekara talatin ba. Gaba d'ayan su suna cikin tashin hankali da gudu mutane su ke fitowa dan aga su waye hadayar wannan shekarar ganin su kowa ya ke son ya yi amma ban da Bisi.

Dan shi tun da su ka bar gidan su lamma

Timi ya ce ya zo su tafi neman hadaya,Bisi ya ce ba za shiba.

Timi ne ya ke tsara masa irin ganimar da ake samu idan ka kawo hadaya.

"Bisi idan ka samo hadaya to K'ainani ma sai ya albarka ce, kuma sai an baka mata a cikin bayin sarki Gannami, yan zu ba ka ga Layo ba matan sa fa sha uku.kuma duk a wajen neman hadaya ya samo su"

Bisi ya tab'e baki sannan ya ce " kai mata su ka dama, dan haka ni bazan je ba"

Timi ne yace"to shikenan gaskiya ba zan biye maka ba, inason mata, dan kai ba kasan su ba ne, dan haka ni na tafi ne ma" gaba ya yi Bisi kuma ya tafi bayan gari ya hau bishiya.

Duk san da ya hau bishiya sai ya yi ta tunanin waye ya yi wannan bishiyoyin, idan ya ga no can k'oluluwan gari kuma sai ya yi ta tunanin su ma k'ainani ne ya yi duk wannan nisan. Zuciyar shi tak'i yar da da hakan duk san da ya ga dabbobi,da tsuntsaye sai ya yi tunani a kan su, gani ya ke kamar a kwai wan da ya yi wad'annan abubuwan.

Dan yan zu ma da aka kamo hadaya baisaniba, ya na can tunani a bayan gari.

Ihu Hazid ya ke yi ya na wulli da dukkan abin da ya ke kusa da shi, tun da ya fara ganin budurwar madubin tsafinsa kullum sai haukansa ya tashi.

Shiwu da kullum cikin zullumi da jiran samun magani ga me da ciwon Hazid ta ke. Jin ihunsa yan zu da yamma lik'is d'in nan shi ya d'aga mata hankali, ga sarki can a d'aki tare da wasu matan ya na aikin da ya saba kullum shine Abu d'aya haka dakarun da su ke kula da shi su ka nufi d'akin na shi. Ganin yadda ya ke fashe - fashe ya sa su ka yi saurin watsa masa sark'a.

Boka 'Dundumi ne ya bayyana cikin d'akin, shiwu da ba ta da nutsuwa ce ta ce " Boka ba ka da amfani a masarautar mu, me ne maganin warakar Hazid ka gayamin ko in sa a fille kan ka?"cikin tsawa ta ke magana da hargagi.

Boka 'Dundumi ya shek'e da wata irin dariya dan yan zu ko da yasan maganin ba zai iya bari Hazid ya warke ba, dan muddun Hazid ya warke burinsa kuwa ba zai tab'a cika ba.

"Shiwu Hazid ba zai tab'a warke wa ba,tun da na ka sa bashi lafiya, to kuwa duk duniya ba wanda zai warkar da shi".

" k'arya ka ke boka 'Dandumi na rantse da k'arfin tsafi da kuma K'ainina sai d'ana ya samu lafiya" sarki Gannami ya katse boka 'Dandumi fitowa ya yi tare da 'yanmatan su na ta ke masa baya.

"Ya shugabana muddin kanason mulkin ka ya dauwama to kuwa ciwon Hazid shi ne makamin ka, idan kuwa kace sai ya warke maganan da bakaso to dole sai ta tabbata" boka 'Dundumi ya tuna masa. Duk da shima ba bare zai yi wad'annan samari su shigo masautar ba.

Shiwu da batasan zancen ba ta taso da sauri tace" jini na fansa ne ga yarima Hazid boka su waye za su ba shi lafiya a ina su ke?.

Boka 'Dundumi ya ce" zuwan su dai - dai ya ke da roshewar masarautarmu, ba mutane ba ne kamar mu,su wasu irin mutane ne ban san me ne madogarar su ba,amma tabbas ba tsafi ba ne"

"A'ina su ke in dai Hazid zai warke, masarauta ba komai ba ce a ga re ni"

Sarki Gannami da furucin da Shiwu ta yi ya ba shi mamaki cikin tsananin rashin imani ya d'auke Shiwu da mari, sandar mulkin sa ya nuna ta take Inda ta ke ya zama zagaye da k'arafuna .

"Ke za ki sa mulki na ya lalace? To kuwa ba zan cireki anan ba har sai kin hak'ura da sanin mayak'an nan da za su zo Masarautar mu".

Obi farin cikine ya kamata ganin Shuwi a Keji. Murmushi ta ke ganin tsafinta ya yi tasiri akan Shiwu tun da har yan zu sarki Gannami ya iya kulleta a d'akin d'anta Hazid. Boka 'Dundumi ne ya ce " ya shugabana ko ni bazan bari su shigo masarautar mu ba.kuma zai warkar da Hazid ko ta wani hali.

Sai yan zu hankalin sarki Gannami ya kwanta.

Kurciyar boka 'Dundumi ce ta sauka a gabansa bakin ta ya na aman wuta a furgice boka ya ce""""""

A cikin garin kuwa sai raye - raye da kid'e kid'e ake ta yi gobe akwai shan roman hadaya kuma wasu za su yi aure a wajen bauta.

Samarin da za'ayi hadaya da su an kai su d'akin da aka tanada don ajiye hadaya a ciki, an tsafacesu ba su da wani tunani ko damuwa kamar dai dabbar da ake samowa a yanka.

Ranar bikin shekara a agarin Duhuwa, kowa cin ado ya ke ya nufi wajen dodon gunki K'AININA.

Lamma da Hantsi ne a d'aki kamar kullum sun san ba za su tab'a ganin irin wannan shagalinba, ba za su sha romon hadaya ba dan tun da su ke ba su tab'a shaba.

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

TSARAWA DA RUBUTAWA

NA

R.HUSSAIN DA NOORY.

□ROYAL STAR WRITER'S ASSOCIATION□*

{R.S.W.A}

https://www.facebook.com/Royal-Star-Writers-Association-101607075594165/?ref=py_c

```MARUBUTA MASU AIKI DA FASAHA DA ZALLAR TSAKWARON AMANA, FAƊAKARWA HAƊI DA NISHAƊANTARWA GAMI DA WA'AZANTARWA HUMMM WANI ABU SAI ROYAL STAR WRITER'S ✍ ASSOCIATION RUWA KAƊAI KE MAGANIN KISHI (R..S..W..A) □□□□

UP-UP-UP```

_"ALKALAMINMU□ YANCINMU"□_

MUNA ALFAHARI DA MASOYAN MU, ALLAH YA BAR ZUMUNCHI□

*LAST FREE* *PAGE*

~LAST FREE~ ~PAGE~

01/02/22



.....✍ Tun da boka 'Dundumi ya d'ora idanunsa akan Bisi ya ji zuciyarsa ta cika da shakkarsa, ganin sa da yayi a tsaye, ga kyau ga cikar haiba, tsarin halittarsa kawai ya ke bi da kallo, ba dan walkin da ke k'ugunsa ba, da abinda zai hana yace ya na d'aya daga cikin samarin da suke farautar MASARAUTAR su,
```

Bisi cikin ladabi ya bud'e hannunsa ya sunkuyar da kai k'asa yace"d'an uwana ba shi da lafiya,ya na fama da ciwon ciki matsananci ka bamu magani boka, K'ainina ya taimakeka".

K'uri ya yi masa da ido sanna 'Dundumi yace" waye kai, da kazo neman magani gurin shugaba".

Cikin damuwa da wannan tambayoyi na boka 'Dundumi yace" nasan ba mai warkarwa sai kai shiyasa na zo, ya shugaba"

Timi da ya gaji yace" boka ka taimakemu yaron ya na cikin tsananin buk'atar maganin".

Boka'Dundumi ya rufe idonsa ya fara surutai, ta ke ya bud'e idon cikin mamakin wani bak'in duhu da ya rufe masa taskar tsafinsa, da alama gaba d'aya al'amuran Bisi ba za su bayyana ba, so ya ke ya ga waye shi amma abun ya k'i bayyana, k'ara bud'e idon ya yi,ya k'ara kallon Bisi da shima ya kafe shi da idanunsa masu ruwan zaiba aciki.

Timi da ya fara hassala dan ya na d'akin amaryarsa, Bisi ya janyo shi, ga shi boka ba shi da niyyar ba su maganin, ya na cikin tunanin ya ji boka yace"Timi d'an Shiya

da Numi, matarka sai jiranka take, za ka haifi d'a namiji nan da wata tara, sunan sa Lashi, ka sa ki ranka yanzu ai zan ba ku maganin ku tafi ".

Timi da tun da aka fara zayyano masa nasabarsa ya yi tsuru - tsuru, jin ansan abin da ke zuciyarsa na jin haushin Bisi ya sa ya saki ransa,kar boka 'Dundumi ya

cutar da shi.

Boka 'Dundumi ya koma kallon Bisi ya k'ara tsafinsa still duhu ne ya bayyana bakomai na Bisi da ya gani, cika ya yi da mamakin wannan al'amari dan bai tab'a ganin abin da ya gagareshi ba kamar maganin Hazid sai sanin waye Bisi.

Tsafi ya yi ya jefawa Bisi dan ganin ko yana da k'arfin tsafi ne,shiyasa ya b'oye komai nasa ba Wanda zai gani.

Ganin Bisi ya na kakkarwa kamar mai jin zazzab'i yasa boka ya gane shi ba matsafi ba ne.

Ya yi mamakin ganinsa, ga shi namiji k'ak'karfa amma ba shi da tsafi a jikinsa, sanin da ya yi na al'adar samarin garin bayan ka yi fansar hadaya to za ka fara neman tsafi ka shirya kanka da shi, dan ko yak'i a kazo musu,ba'a ganinsu b'acewa su ke yi.

Sai da ya gama jijjiga Bisi,sannan ya ba su maganin, da gudu Bisi ya d'iba dan gani ya ke kafin ya koma Hantsi ta mutu, Timi da ya ja tsaki" mtsww ya san ba tsayani zai yi ba,ya fito da ni kuma ya barni,anan"

Kamar an jefo shi haka ya shiga gidan wajen tulunsu ya nufa,ruwa ya d'ebo ya zuba a wani fafaffen snail(dodonkod'i).

Ya shiga d'akin su Hantsi. Rona da ta ke binsa zugui -zungui ba magana haka su ka shiga d'akin Hantsi da ke kwance a jikin Lamma,tayi zuru - zuru da ita,sai sannu suke faman yi mata, d'ago ta Bisi ya yi,ya zuba garin maganin a ruwan take ruwan ya fara hayak'i nan da nan ya zama kamar ruwan zafi, a baki ya bata ta sha, ta na gamawa sai amai, su na ganin tayi amai su ka fara murna su na cewa"K'ainina ya hak'ura ya dawo mana da ita"

Bisi ya yi murmushi yace"ai ba yanzu zai d'auke ta ba,sai ta zama kamar ki Rona ko ma ta fiki"

Su ka shek'e da dariya har ita Hantsin,take kuma ta mik'e kamar ba ita ke suma ba.

Prince Prov

Prince Zaid su na fitowa daga sallah tare da mahaifinsu,da Safwan. Malam Ibrahim sarkin dawakai ne ya dunk'ule hannu ya na kai gaisuwa ga sarki da su Prince Zaid. Mai martaba yace" a tambayi sarkin dawakai akwai matsala ne?"

Wani dogari ne yace" su Yarima sun amsa, akwai matsala ne?".

Cikin k'ara russunawa yace"ranku ya dad'e doki ne tun da safe ya ke ta haniniya, can kuma sai ya ke wani irin kuka,shi ne nake neman izini in kira likita ya duba shi".

Prince Zaid tun da yaji ance doki ya nutsu,dan a duniya ya na k'aunar doki,ta ke yace wa mai martaba"ranka ya dad'e ina son zuwa na ganshi".

Sarki Abdurrahman yace"Zaid ka bari zuwa gobe in Allah ya kaimu mana"

Cikin nuna k'aunarsa da doki yace"a yimin izini Abbana" sarki ya yi murmushi yace"kaji ance masoyinka ko,ai shikenan kaje".

Prince Zaid da sauri yace"godiya nake ranka ya dad'e, sanna ya cewa dogarin "a cewa malam Ibrahim ya kai shi wajen dokin".

Sarki Abdurrahman ya shiga fada,dogarai su na ta kareshi dan ko tafiyarsa ba'a gani,Prince Safwan kuwa so ya ke ya shirya dan anjima akwai zuwa club caso, part d'insa ya wuce domin shiryawa kafin su yi sallar magriba da isha'i, dan duk son rayuwarsa ba ya baya barin sallah ta wuce shi.

Malam Ibrahim (baban Zeenat) ya wuce domin nu na wa Prince Zaid dokin, su na shiga gidan dokin ya ga dokuna sun kai ashirin ya yi mamakin dawakan nan wannan bawan ne kad'ai yake kula da su.

Wani farin doki mai kyau ya nuna masa yana cewa"Ranka ya dad'e gashi nan" ya na matsawa baya, ya na durk'usawa.

Kusa da dokin Prince Zaid yaje, tab'ashi ya yi ya kara kunnensa a daidai wuyansa,sannan ya sa hannu, can ya d'auke, sai ya bud'e idon dokin murmushi ya yi yace" ku ba ni paper da biro" ta ke wani bawa ya fita a guje don memo biro da takarda, bai jima ba kuwa ya kawo"ranka ya dad'e gashi " ya na mik'awa.

Take prince ya rubuta magani yace a siyo a bawa dokin ya sha, sai shafa dokin yake dan yayi masa kamar dokinsa (Don) .

Sannan yace a ware shi daga cikin dawakai idan ya warke, asanar da ni" juyawa ya yi dan ficewa daga wajen,bayi su ka rufa masa baya.

Fulani Samira da ke yau ita ce da mai martaba, sai hura hanci take ta na cika ta ba batsewa ita ga matar sarki. Khalil d'an autanta ne a zaune ya na ta buga game a wayar

Fulanin, kallon yaron ta yi da bai wuce shekara bakwai ba, ta yi murmushi tace"ko sunk'i ko sun so,sai ka zama sarkin MASARAUTAR MU, wannan alk'awari na ne".

Princess Firdausi ce ta fito,rik'e da carbi ta na azkar d'in yamma tace" Mama ina sury?" Fulani ta kalleta sannan ta tab'a baki ta je shan iska ne 'yar sarki ce fa ko so kike ta zama kamar 'yar malam yadda ki ka mai da kanki mtswww" ta k'arasa da tsaki.

Princess Firdaus tace" sorry mah naga ta dad'e ne" daga haka ta koma d'akinta dan sarki Abdurrahman bai yarda da warewa yaransa mata part ba.duk da part d'in ya na nan amma ba kowa a cikinsa, ya tanade shi ne saboda gaba, kuma ko wacce ta na da bayinta. A yanzu haka.

Firdausi ta na karanta political science anan k'asar cikin Maryam Abacha University ba kowa ne yasan ita 'yar sarki ce ba ce,ta na shiga cikin mutane ba ta da wulak'anci da tak'ama, sai dai akwai mulki, dan sarauta a jininsu take.

Surayya kuwa yanzu ne ta gama secondary d'in ta, tace ita a Europe takeso ta yi karatu.

Duk wani hali da d'abi'a ba inda ta bari mahaifiyarta Samira, ta tsani talaka bayinta ba k'aramin wulak'anci su ke sha ba.

Jakadiya tun sassafe ta ke neman Shamsu dan tsohon d'an bori ne,ba aljanin da baya hawa. Shine ya san inda zai samu mata boka buzu ya ke zaune. Dan yanzu ta kwan biyu ba ta je ba. Ganin Shamsu ta yi yana zaune ya na shan taba, da sauri ta k'ara sa wajensa tana cewa" kaga mazan jiya, kaga mazan yau, kaga masu duniya da abin da ke cikinta, mu samu a duniya lahira kuwa sai mai rabo" "hahhhh hahhhhh nagode Jakadiya k'auren fada me kike da buk'ata ne " Shamsu ya tambayeta ya na d'aukar goro ya na ci.

"Yauwa d'an gari" Jakadiya ta fad'a ta na lallek'a lungu da sak'o, dama da hagu san nan tayi k'asa da murya tace" gidan boka buzu za ka rakani shamsu" wani kallo ya yi mata sannan yace " a nawa zan kai ki?" Daman tasan halin sa ta zaro kud'i zasuyi dubu goma ta mik'a masa.

Saurin karb'a ya yi yasa a aljihu sannan yace"ki shirya da daddare mu d'au hanya,dan ya na can wani daji kuma da nisa tsakaninmu da shi".

A haka su ka rabu za su had'u a kofar baya sai su wuce.

BILKISU PROV

Hibbullah yace"ba ki ji abin da Daddy yace ba ne,ki bari sai gobe?"

Bilkisu da hawaye ya fara sharara a fuskarta ta zube a kusa da Waziri dan Allah Daddy ka bar ni naje idan ban je ba zai ga kamar na wulak'antashi kasan shak'uwar mu tun mu na yara".

Waziri da yasan haka sai ya ce to ki bari da daddare sai Yayanki ya raka ki kinji" ba dan ta so ba ta hak'ura dan Hibbu ya na nan kar ya ga tayi ba dai - dai ba.

Cike muke a k'ofar fada kowa ta na tunanin a ina za mu kwana kafin safiya yarima ya zab'i bayin da za su yi masa hidima.

Ummata ta kasa tafiya ta bari tace"Zeenatu kinga ba ki da cikakkiyar lafiya, ki kula kafin safiya mu zo muga abin da halin zai yi".

Cikin sanyin jiki nace " yanzu shikenan anan zan kwana Umma,gurin akwai sanyi inhaler na ta na gida,kar asmana ta tashi acikin sanyin nan ga k'ura" hawaye ne ya zubo musu abin gwanin ban tausayi.....

Ki biya ki *karanta cikin* *kwanciyar hankali,

Ki sa ni ALLAH BAYA YAFE HAKKIN *WANI AKAN* *WANI*

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

TSARAWA DA RUBUTAWA

NA

R.HUSSAIN DA NOORY.

□ROYAL STAR WRITER'S ASSOCIATION□

{R.S.W.A}

https://www.facebook.com/Royal-Star-Writers-Association-101607075594165/?ref=py_c

```MARUBUTA MASU AIKI DA FASAHA DA ZALLAR TSAKWARON AMANA, FAƊAKARWA HAƊI DA NISHAƊANTARWA GAMI DA WA'AZANTARWA HUMMM WANI ABU SAI ROYAL STAR WRITER'S ✍ ASSOCIATION RUWA KAƊAI KE MAGANIN KISHI (R..S..W..A) □□□□

UP-UP-UP```

_"ALKALAMINMU□ YANCINMU"□_

DEDICATED TO YOU MY LOVELY SISTERS MAMAN ARIFULLAH (RAYUWAR IRFAN) KYAUTAR ALLAH (K'ANWATA)

AND

MAMAN HANEEF(AKI'DAR MASARAUTAR).❤
```

LITTAFIN KU'DI *NE , KI BIYA KI KARANTA CIKIN* *AMINCI*

2414444137

Zenith bank

Rahinat Hussain

Ki tura shaidar biya ta wannan number 08107916039.

Idan kuma katin waya ne zaki tura katin MTN d'in ki ta wannan numbers d'in 08107916039 ko 08145498489.

Free pages ya kusa k'arewa ki yi k'ok'ari ki biya ki karanta ba tare da cin hak'k'in wasu ba.

.....✍ Lukman da ya ke part d'in Prince Zaid ya hana kowa yi masa komai, dai-dai da had'awa Prince Zaid ruwa a toilet shi da kansa ya yi masa, hira ya ke masa yana ta gaya masa yadda abubuwa ke tafiya a cikin MASARAUTAR, sanin halin Prince Zaid ba damuwa ya yi da harkar sarauta ba yasa Lukman yin shiru.

Prince Safwan ne ya shigo tare da bayinsa, tsayawa su ka yi a k'ofar part d'in domin ba su da ikon k'arasawa ciki.

Ya na shiga ya ga yadda aka ajiye abincin da aka kawo masa haka ya ke, abin da ya kawo shi kenan, Fulani mahaifiyarsu ta sa d'an uwansa ya duba idan bai ci ba yasa ya ci, dan akwai alkunya tsakaninta da Prince Zaid a matsayinsa na d'an fari, dan ma yanzu ta na ragewa idan ba idon mutane.

Prince Safwan na shiga ya ga Lukman ya na mik'amasa apple domin ya d'anci dan sallah ya ke so ya yi dan har uku saura bai yi ba, kasan cewarsa mutum mai dad'ewa a wanka sai ya yi hour bai fito ba.

"Assalamu Alaikum"

Safwan ya shiga da sallama jin muryar d'an uwansa ya sa shi sakin murmushi, shi dai yana k'aunar Safwan halinsa ne kawai bayaso, na kula 'yanmata,da son rayuwar holewa.

Lukman ma murmushi ya sakar masa ya na tsine masa a ransa, dan yasan tunda Safwan ya shigo to kuwa dole ya yi ka rar barin d'akin dan su yi hirar yaushe gamo,kamar yadda shima ya yi a yanzu.

Cewa ya yi"wa'alekumussalam da yarima k'arami" Safwan yace "to zaka fara kenan dan ka ganshi ko?"

Lukman cikin fara'a yace" ai dai haka sunan ya ke ko ba haka ba Prince? "

Prince Zaid murmusawa kawai ya yi, Prince Saff ne yace" ai da ba wani Yarima Kʻarami da kake cewa, Yarima kawai ka ke cewa,dan yanzu ka ga bross shine wani har da Kʻarami".

Dariya Lukman da Saff sukayi, shi kuwa Prince ko murmusawan ma bai yi ba. Dan baya son hayaniya sosai.

Lukman ne ya ce "to ba ri in barka ka huta bross, Saff sai ka fito" ya fad'a ya na kallon Saff d'in da ya zauna kusa da Yayan nasa.

Prince Zaid ne yace" Safwan ina fatan komai normal ko, ka k'ara hankali ai yanzu da gani ma ansamu canji"

Cikin shagwab'e fuska yace "haba bros ni fa yanzu Ustaz ne, har na fi sheik Sudees d'in ka" dukan wasa ya kai masa yana cewa" haba dai ai na san ko shekara d'ari za kayi, ka na karatu ba za ka kamo ya sheik ba".

Dariya sosai Safwan ya yi sannan yace"Mommy ce ta ce lallai - lallai inzo in ciyar da kai abinci,dan tasan halinka tun kana cikin ciki" Prince Zaid da ya ga Safwan ma ya

k'ara rainashi a wannan zuwan ma.sai cewa ya yi"ba na son rashin kunya Saff,zan zane ka yanzun nan".

Sanin Yayan nasa baya son yawan hayaniya ne yasa yace"tuba nake babban Yaya bari in d'auko maka abincin".

Ya na janyo kayan abincin Prince Zaid ya mik'e ya tayar da sallah sai da ya d'au lokaci yana addu'o'i da neman yafiyar Allah sannan ya zauna ta re su ke cin abincin dan ya ci dayawa ne Saff ya ta ya shi.

Jin motsin k'ofa yasa su ka kalli wajen ganin yan zu kuma ba su ji ba yasa su ka mai da hankalinsu su na hira,kiran sallar la'asarne ya sa duk su ka mik'e domin zuwa masallaci. Tare su ka fito abin sha'awa da su,kowa ya gansu sai sun burgeshi, zubewa kawai ake ana kwasar gaisuwa, Saff ke d'aga hannu amma prince kamar baisan da mutane ba, dan shi har ga Allah baya son wanna rayuwar, ganin manya da taofaffi sai durk'usa musu su ke.

Lukman na fita ciki part d'in sa ya wuce, duba hannuwansa ya ke yana cewa " kamar yadda na ke ciyar da kai da hannuwana haka zan halaka ka da hannuwana, da ga kai har 'yan uwanka Zaidul'abideen Abdurrahman Abdul'azeez hahhhhahhh"

'Bangaren Fulani Hafsat kuwa laulayin k'arya ta ke tayi sai wahalar da bayinta ta ke, ke dafa min wake da attaruhu, ke aje a nemomin aya mai gishiri haka su ka wuni sintiri daga wannan sai wannan, kuma idan sun kawo ba wanda ta ke ci, sai ta ce a fita da shi ba ta so.

Mai martaba ma sai sintirin zuwa part d'inta ya ke dan ba k'aramin farin ciki ya yi da samun cikin Hafsa ba, dan yana tsananin tausayinta tunda ta samu cikin nan ya ke kyaututuka kala kala. Ya sa malamai ayi ta addu'a Allah ya inganta mata, ita ma ta ga d'anta a duniya.

Ganin Lukman har yanzu bai shigo part d'inta ba ya sa ta kira wayarsa Ringing biyu ya d'aga ya na kwance a kan gadonsa ya na jin k'iyayar mutanen MASARAUTAR MU, dan har sarkin jin tsanarsa ya ke duk da ya d'auke shi d'a kuma ya na rik'eshi tsakani da Allah.

"Hello Aunty"

Daga can Fulani Hafsat ta ce"Lukman kana ina tun d'azu fa ban ganka ba".

Lukman yace"ina part d'in Zaid yanzu na fito lafiya?"

Da sauri ta mik'e tsaye tace" part d'in sa kuma, me ka yi masa sai kace wani bawansa?"

Murmushin mugunta ya kuma yi sannan yace"bawansa ne mana Aunty a zahiri,a bad'ini kuma ajalinsa ne"

Dariya ta shek'e da ita "hahhhh ina son ka d'ana, kai kad'ai ka sharemin hawayen rashin haihuwa Lukman".

Shigowar su princess Firdausi da k'annenta ne ya sa Hafsa ta yi saurin yanke wayar a diririce tayi yak'e ta na.....

* * * *

Kuka nake kamar ance zan bar duniya, Umma ce ta ce" yanzu Zeenat ba za ki k'arfafa mana guiwa ba, kin san idan ba mu kai ki ba ba mu kyauta wa sarki mai adalci ba, nima hak'uri nayi kuma mahaifinkima shi ya yi, ki zo muje idan Allah ya sa ma ba'a zab'e ki ba ma, shikenan mun dai yi biyayya ga shugaba ko"

Da wannan bayanin na Umma na, naji nutsuwa kuma ai ba wai MASARAUTAR MU zan bari ba gaba d'aya, kwana ne kawai bazan dinga yi a gidan mu ba, amma nasan kullum zan iya ganinsu, in ba ni da aiki.

Baba ne ya k'ara da yimin nasiha "Zeenatu ki yi hak'uri haka Allah ya haliccemu a bayin tun iyaye da kakanni, kakana ma shine sarkin dawakai haka mahaifina, har zuwa ni kaina.

Cikin shagwab'a nace" nima sarkin dawakai zan zama?"

Gaba d'ayansu daga Umma har Baba sai da su ka yi dariya. Su na jin rashin dad'in rabuwa da 'yarta su ko dan shirmen ta ma sun San za su yi kewarta.

Haka aka dinga fita da 'yan mata ana kaiwa fada, dan da safe Yarima zai fito zab'ar bayin da za su dinga yi masa hidima a b'angarensa.

Had'uwa na yi da Fatima wadda ita hankalinta kwance addu'ar Allah ya sa a zab'a da ita take tayi, ni kuwa ina addu'ar Allah ya sa kar a zab'e ni acikin bayin sa, dan dagani ba shi da mutunci kuma ni ba zan d'auki wulak'anci ba...

* * * *

Sheik Usman ne ya ke yiwa Harun nasiha dan gobe ne jirginsu zai tashi da asbah zuwa india dan shi yana karan tar physiotherapy Harun akwai boko Sudees kuwa both side Arabic da boko sai dai ya fi son harkar JIHAD DA'AWA FOUNDATION d'in sa, duk da in yana ba da karatu ka kawo masa assignment d'in ka ko project to kuwa cikin hukuncin Allah sai kasamo abin da kake so, dan sudees he is brilliant person.

Sai da kowa ya k'ara yiwa Harun nasiha daga sheik Usman gadon k'aya har Umminsu da Sudees sanan kowa ya tafi makwancinsa.

Harun ke waya da budurwarsa ba shi ya kwanta ba sai wajen k'arfe d'aya na dare.

SULTANA PROV

Mahaifin Sultana Ambassador Bashir ya k'ara shiga falon,da gudu 'yartasa tilo ta fad'a jikinsa ta na k'ara runtuma ihu" Daddy ka auramin Sudees, idan ban same shiba mutuwa zanyi" saurin rufe mata baki ya yi yace"please stop crying daughter, na miki alk'awarin za ki aure shi,ni da kaina zanje in sami Sheik Usman d'in kinji?"

Kai ta d'aga ta na share hawayenta,sannan yace" jeki ki kwanta ki huta kar kanki ya yi ciwo" tafiya tayi ta haye sama, Iyayen nata su ka bita da kallo.

"Haba Hajiya ya za ki ka sa shawon kan ''yar wannan matsalar a matsayinki na uwa?" Ambassador Bashir ya ke fad'a.

Hajiya tace"to Alhaji yaron nan ba sonta ya ke ba,amma ta nac..." Ke dakata Wallahi sai ya so my daughter, shegen yaro mai taurin kan tsiya,duk ya mallake zuciyoyin jama'a ya rubuce ya shanye kowa k'aunar had'a zuri'a da shi ya ke kuma yak'i auren 'ya ta,to kuwa k'arya yake bai isa ba" fuuuuu ya wuce stairs, Hajiya tace "Allah ya kyauta".

Sultana tunda ta kwanta a gadonta wayarta ta d'akko pictures d'in Sudees ta ke ta kallah tare da videos d'in tafseer d'in da yake, hasasoshi ta ke aranta yadda zasu zuba love idan sunyi aure.....,...

To ko ya zata kasance??????

Littafin kud'i ne,ki biya ki karanta.

ALLAH ba ya yafe hak'k'in wani akan wani.

[4/3, 9:00 AM] Aisha Bauchi: □□□□□□

MASARAUTAR MU

□□□□□□

TSARAWA DA RUBUTAWA

NA

R.HUSSAIN DA NOORY

□ROYAL STAR WRITER'S ASSOCIATION□*

{R.S.W.A}

https://www.facebook.com/Royal-Star-Writers-Association-101607075594165/?ref=py_c

```MARUBUTA MASU AIKI DA FASAHA DA ZALLAR TSAKWARON AMANA, FAƊAKARWA HAƊI DA NISHAƊANTARWA GAMI DA WA'AZANTARWA HUMMM WANI ABU SAI ROYAL STAR WRITER'S ✍ ASSOCIATION RUWA KAƊAI KE MAGANIN KISHI (R..S..W..A) □□□□

UP-UP-UP```

_"ALKALAMINMU□ YANCINMU"□_

WANNAN LITTAFIN NA KUDI NE IN KINGANSHI A WAJE, KI BIYA KI KARANTA CIKIN AMINCI

NORMAL GROUP N300

VIP N500



.....✍" wayyo!wayyo!! K'ainina ka sa Hazid ya sa ke ni da wannan ciwon,na tuba ba zan k'ara cutar da Shiwu ba" Obi ce da jikinta ya fara neman rub'ewa ta ke ta sambatu cikin jin tsananin azaba.

Sarki Gannami da yanzu ba ta ita ya ke ba,ta wasu yara da ya k'ara aurowa a bikin shekara ya ke, Hazid ya k'i kowa yace matarsa za ta zo gare shi.
```

Shiwu da fadawanta ne a zaune su na jiran Hazid dan ta na tausayin halin da Obi ta ke ciki, ta tanadar ma sa giya domin ta shawo kansa ya karya tsafin da ya yi. Dan boka 'Dundumi ya k'i yarda ya karya dan burin sa shine ya cusa musu k'iyayyar junansu a cikin MASARAUTAR , ta yadda lokaci d'aya zai koma shugaban MASARAUTAR MU.

"Ki bayyana a gareni, ina matuk'ar k'aunarki kin hanani jin dad'in rayuwa, na dai na kula mata,ba daina samun sukuni, duk in da ki ke na rantse da furfutar kan kakana, sai na nemoki" ihu ya k'wala ya fita a guje ya yi cikin gari.

Take 'yan mata su ka fara gudu dan ceton rayuwarsu.

Wata yarinya ya rik'e ihu ta ke tana neman taimako dan tasan mutuwa za ta yi cikin hauka Hazid ya ja ta a k'asa ana ji ana gani ya lalata ta, ya murd'e mata wuya ta ke a wajen ta mutu, kuma ya na cikin gushewar hankali duk in da ya kalla budurwar cikin mudubi ya ke gani.

Sarki Gannami ya na jin abin da Hazid ya yi ya bushe da dariya"hahhh hahhhhh Hazid kenan K'ainina nasan ya na alfahari da kai, a nemo boka 'Dundumi ya zo ya dubamin Hazid nasan izuwa yanzu ya gano maganin"

Boka da ya ke jin abin da ya ke faruwa take ya bayyana, cikin mummunan shigarsa na walki baki anjera masa idanun mujiya k'ulle - k'ullen layu ne a wuyansa da hannayensa.kansa kuwa duk yayi fari ba bu ba'kin gashi ko d'aya akan sa.

Hazid da ya ke ta ihu a d'aure dan idonsa kawai budurwar cikin madubi ya ke hasko masa,shiyasa ya ke ta ihu yana cewa" ki zo gare ni zan jiyar da ke dad'in duniya, za mu yi mulkin MASARAUTAR MU ni da ke, ki zo kafin na nemo ki da kaina, na rantse da K'ainina muddin na ganki, sai na d'and'ana miki azaba mai rad'ad'i, sai na shayar da ke d'acin da nakeji a zuciya ta "

Boka 'Dundumi ya ke ce da dariya, cikin muryar 'yanmata yace" hahhhhhh Hazid za ka aure ta, wace ce wannan".

Shiwu da ta ke ta kuka tace"yace a madubi kawai ya ke ganin ta,mu bamu tab'a ganin ta ba, ko a mudubin ma, boka ka taimake mu haukan sa k'aruwa ya ke"

Had'e rai boka 'Dundumi ya yi yace" na gayamuku warkewar Hazid dai - dai ya ke da rasa MASARAUTAR MU, amma kullum zancen ki d'aya Hazid ya warke, zai warke amma sai in mun bar samarin nan sun shigo, kuma shigowarsu garin Duhuwa rasa MASARAUTAR MU za mu yi, za mu zama ba yi k'as.....

Ya isa "'Dundumi!!! Hazid zai warke,kuma ba za mu tab'a barin su su zo ba, yanzu ka yi masa magani ya dai na illata kansa" cikin tsawa da muzurai sarki Gannami ya fad'a wa boka.

Shiwu da ta ke kallon Hazid a halin hauka,ta ce "ni meye ne K'ainina ya ke so mu yi,ya warkar da shi, mun yi duk abin da yakeso,hadaya ma ya ji dad'in ta,amma ya ka sa yi mana wannan".

Boka ne ya fara fitar da wani irin hayaki ta bakinsa take hayak'in ya cu re waje d'aya Hazid da ya ke ta ihu hayak'in ya nufi in da ya ke zagaye Hazid ya yi take haukan ya ta ci,ya dawo hayyacinsa.

Bisi ne tsaye akan bishiya ya na ta kallon yadda tsuntsaye su ka sak'a shek'arsu da k'wayayensu a ciki, kallon su ya ke yana tunanin su ma k'aininan ne ya yi su kenan, zuciyarsa ta k'i aminta da hakan amma dole ya yarda.

Gari ne ya rufe saboda hadari da ya taso, Bisi bai kula da hakan ba, yana ta tunani,sai ruwa da sauri, ya sauko daga kan bishiyan ya na neman hanyar gida.

Wata bukka ya gaji da sauri ya shigo ciki daga gefe ruwan sama ne ya taru kallon sama ya ke yana tunanin ta ina ruwan nan ya ke zubowa shima K'ainanin ne ke ba su?" Kullum tunanin bisi kenan.

Sai da ruwan ya d'auke ya fito ganin garin ya yi shiru ba kowa, haka ya k'a ra sa gidansa, wani tsoho ne kwance ya na jinya shi kad'ai ne a cikin gidan. Gurin tsohon Bisi ya je yace" Ayo ya jikin" tsohon da ya kafe Bisi da ido ya yi murmushi yace"da sauk'i Bisi yau kuma ina kaje?"

Cikin nuna gajiya yace"ina wajen yawo a can ruwa ya tare ni ai".

Tsohon da ya ke son bayyana wa Bisi wani sirri amma ya na tsoro, kuma bayaso ya mutu bai fad'i wannan sirrin ba.....

Sudees prov.

"Ina jin ka Hamza, me ke tafiya ne a can Moroccon?" Sudess ke waya da Hamza.

Hamza cikin juriya irin na wad'anda su ka mik'a kansu ga Allah, ko a kashe su ko su,su kashe zuciyar da gaske ta ke yace" Alhamdulillah da alama akwai nasara dan garin ba su da yawa kuma gaba d'aya ba su da wani addini haka su ke rayuwa kamar dabbobi Wallahi Sheik" cikin jin ba dad'in yanayin da su ka gansu.

Ajiyar zuciya Sudees ya sauke yace"Allah ya taimakemu ya ba mu rinjaye akansu, ina nan zuwa Insha Allah " da haka su ka yi sallama.

Ya na ajiye wayar kiran Sultana ya shigo kamar ba zai d'auka ba sai dai ya d'auka"Assalamu Alaikum warahmatullah "

Daga can kuwa Sultana ce cikin muryar kuka tace"wa'alekumussalam ya Sheikkkkk"

Jan sunan ta yi saboda ta yi masifar mutuwa akan son sa, shiru su ka yi na d'an lokaci,sannan tace "ya sheik dan Allah ka yi hak'ura idan na takura ma ka".

Cikin nu na k'osawa yace bakomai" idan tambaya ce, rubutowa za ki yi ba kira ba,nagode"

Katse wayar ya yi yana tashi don zuwa su yi hira da Umminsa.

Sultana na jin ya katse wayar k'ara rushewa da kuka ta yi,tana cewa" Sudees Wallahi dole sai ka aure ni tunda Daddy na yace sai ya aura min kai"

Daga can kuwa Ambassador Bashir ne ya kira Sheik Usman gadon k'aya,gaisawa su ka yi sannan Ambassador Bashir yace"Allah gafarta daman ina so na zo ne,akan wata muhimmiyar magana".

Sheik Usman ya yi murmushi cikin dattako yace"to Alhaji Bashir yau she kenan?"

Alhaji Bashir yace"ya sheik ai kai za ka fad'a"

Sheik Usman yace"to shikenan ko zuwa gobe ne idan muna raye ka iya zuwa" da haka su ka yi sallama cikin girmamawa.

Sultana ce ta ke ta a mai,da gudu mummy ta shigo jin kakarinta, toilet d'in ta shiga ta ta rik'e ta sannu ta yi mata, wanke bakinta ta yi, d'agowar da za ta yi ta kawai ta fad'a jikin mommy a s.....

Rona ce ta shigo dan ta sanar da su za ta wuce shigar ta d'akin kenan ta ji shigowar mutane juyoyar da zatayi idon ta ya fad'a cikin idon.....

Ku kasance ta re da alk'alin R.Hussain da Noory dan jin yadda za ta kaya